🌻 *THE WORLD MAN*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK 1*

*PAGES*0️⃣1️⃣➡️0️⃣2️⃣

Tafiya sukeyi cikin nutsuwa suna hira su biyu Hauwa'u ta kalli Inteesar tare da cewa"Inteesar gaskiya ina ganin musamu wani gurin mu fake saboda naga hadari na niyyar tasowa ke sarkin mura".
"toh yanzu a ina zamu fake anan gurin".
"kinga wata rumfa can muje muɗan fake in ruwan ya ɗauke semu wuce gida".
"toh".
nan suka ƙarasa rumfar wani me shayi suka zauna zamansu keda wuya ruwan sama ya kece aka shiga ruwa kamar da bakin kwarya.

Andaɗe ana ruwan sannan ya ɗauke suka tashi suka cigaba da tafiya sunyi nisa sukaga wasu motoci ƙirar Land cruser baƙaƙe se ta tsakiyar data ƙasance roice-roice fara tas me baƙin tintac motar itace ta cikon ta bakwai wato dai ma'ana a tsakiya danno kai sukayi sunzo wuce daidai su Inteesar bazato sukaji ruwan taɓo da kwatami ya watsomusu a jikinsu sakamakon motar fallatsamusu da tayi cikin sauri da zafin zuciya Inteesar ta wawuri wani dutse dake kusa dasu ta jefi ɗaya daga cikin motar dutsen be tsaya akan kowacce motaba se a glass ɗin farar motar nan ta tsakiya tass kakejin ƙarar fashewar glass ɗin a razane Hauwah ta kalli Inteesar tare da kallon motocin tace"nashiga uku Inteesar kinsanko motar wa kika fasawa glass kuwa?".
cikin masifa wadda ita kanta batasan tanada itaba tace"ko motar waye ina ruwana meyasa su masu kuɗi basusan darajar ɗan Adam ko cemusu akayi muba mutane bane ke bakiga abinda sukayimana ba ruwan kwatamifa suka fallatsamana kina kallo kuma ko niyyar tsayawa basu da ita amma ke saboda rashin kishin kai yasa ki cemun wai nasan motarwa na fasawa glass ina ruwana ko wayemana ai tare suke".

Jin ƙarar glass yasashi ɗagowa daga karatun daily thrust ɗin da yikeyi tare da zubawa gaban motar da yike ido wow na furta sakamakon ganin haɗaɗen matashin guy ɗin yagaji da haɗuwa komai nashi abun burgewane saurin fita drivern yayi bejimaba ya dawo cikin girmamawa yace"Oga wasu yarane kan amfallatsamusu ruwan taɓo shine ɗaya daga cikinsu tayi jifan amma gashi can su Muhd sun zagayeta".
cikin muryarsa da kamar ammasa dole yace"buɗemun mota".
"angama ranka shidaɗe".
nan drivern ya buɗemasa a hankali ya zura ƙafarsa waje yafita cikin takun zaratan maza masuji

da class yaƙarasa gurin wanda hakan yayi daidai da ɗaga hannun Muh'd ze wankawa Inteesar mari.
a ɗan daƙile NAMIJIN DUNIYA yace" Dakata Muh'd".
yaƙarasa maganarsa tamkar wanda aka tilastawa
Wani ƙasƙantaccen kallo me cike da zallan ƙyama da wulaƙanci yake jifanta da shi Cikin lion voice ɗinsa yace" ke Waye Ubanki da me kike gadara da har zaki fasamin glass ɗin motana ubanki waye a ƙasarnan".
Lokaci ɗaya Idanunta suka rine saboda tsananin ɓacin rai saboda dukda suke talakawa batason a wulaƙantamata iyaye a zuciye tace "Da Uban da kake gadara dashi nake gadara mutumce kamarka".
Azuciye ya ɗaga hannunsa da niyyar yarfa Mata mari yaji an riƙe Murmushi ta saki me cike da takaici da ƙunan rai tace" daka mareni tabbas da ka aikata kuskure mafi muni atarihin Rayuwar ka idan har ka yadda wannan wulaƙantaccen hannunka ya taɓa tsaftacciyar fuskata ta".
ta faɗa tare da yin wurgi da hannunsa Bata jira Jin abinda zeceba ta finciki Hannun Hauwa da jikinta keta rawa suka bar wajen.

Hannu yasa ya hargitsa tulin sumar dake kansa kana ya furzar da iska me zafi daga bakinsa wani irin tsuma jikinsa keyi yayinda jijiyoyin kansa suka tashi ruɗu-ruɗu dasu tabbas tunda yake babu wani mahalukin daya taɓa muzantashi irin wannan bagidajiyar yarinyar tamkar ze tashi sama ya juya yashi ɗaya daga cikin motocin guard ɗinsa kafin yaƙarasa sun buɗemasa ƙofa shiga yayi tare da lumshe sexy eyes ɗinsa yayi da sukayi ja dasu tare da furta "senayi maganinki ko ƴar waye harni NAMIJIN DUNIYA za'ah samu wata dirty girl zata gaggayamun magana nayi alƙawari sekinyi regreting ɗin abunda kikayi ".
yana wannan zancen zucin har suka isa wani tanƙamemen building dogo kallo ɗaya zakayiwa haɗaɗɗen building ɗin ka fuskanci ma'aikatace saboda mutane daketa hada-hada a gurin suna gama parker motocin Muh'd yace"Oga mun iso".
buɗe lumsassun idanunsa yayi da sukayi ja ya kalli handle ɗin ƙofa alamar a buɗemasa buɗemasa Muh'd cikin takun ƙasaita haɗe da jiji dakai ya fito ma'aikatan dake gurinne gabaki ɗayansu suka shiga gaidashi ba tare daya amsaba yashiga tafiya saboda tsananin ɓacin ran da yike ciki be zame ko inaba se gurin elavatorn da shikaɗai yike hawa ya danna yashiga ya rife a hawa na goma elavatorn ya tsaya tare da wangale ƙofar fita yayi tare da nufar wata haɗaɗɗiyar ƙofa yashiga nan take wani haɗaɗɗen guri ya bayyana se wata mata datasha atarch akanta yare-yare fuska tasha mai ga heavy make up data cika fuskarta dashi tana danna waya ta bayyana tana ganinshi ta ƙara gyarawa cikin ƙissa tace"Oga sannu da zuwa".
be amsamataba hakan yasa tagane yau yana cikin ɓacin rai dan haka takama kanta tare buɗemasa ƙofa yashiga tanƙamemen office ɗinsa daya gaji da haɗuwa kallo ɗaya zakayiwa office ɗin kasancewa kuɗi sun zauna domin komai na more rayuwa akwaishi zama yayi sakatariyarsa daketa kwarkwasa tashiga zayyanemasa shadul ɗin ranar jingina yayi da kujerarsa tare da lumshe ido fita sakatariya Zeezee tayi bata jimaba se gata da wani haɗaɗɗen cup a hannunta taƙarasa gaban table ɗin da Namijin duniya ke zaune tace"sir your copee is ready".
ba tare daya buɗe idoba yayimata da nuni data bashi miƙamasa tayi ta juya a hankali yashiga shan copee lokaci ɗaya yaji wata nutsuwa tazomasa ya aje cup ɗin tare da danna wayarsa

yayi dialing wata number bugu ɗaya aka ɗauka daga ɗaya ɓangaren wancan yace"Oga ɗiyar massenger ɗin Sir Ahmad ce".
wani murmushin gefan baki Abdallah Namijin duniya yayi ba tare da yayi maganaba ya kashe wayar tare da tura text ya jingina da kujerarsa yana tinano irin abubuwan daya tanazarwa Inteesar.

Ɓangaren Inteesar ko suna barin gurin Hauwa'uh ta kalli Inteesar tace"nifa tsoro nikeji saboda nasan NAMIJIN DUNIYA baze taɓa barinkiba Inteesar meye danya watsamana ruwa".
"gaskiya duniya ba gaskiya wato shi bakiga abinda yayimanaba saboda yanada kuɗi seni nawa kika gani ba wani tsoronsa da zanji ai mutum ne shina kamar kowa kodon kina sonsa shiyasa kike kareshi".
"ba haka bane ƙawata kawaidai……".
saurin dakatar da ita Inteesar tayi tare da cewa"dame kikeso naji da baƙincikin gidanmu koko dana irin wa'innan watsatstsun mutanen da basusan darajar ɗan Adam ba".
"ya haƙuri ƙawata".
suna wannan zancen suka iso gidansu shiga gida tayi itama ta shige gidansu.

Kamar kullum Inteesar nashiga gida ta tadda su Uwar Gwarama da maƙarrabanta a tsakar gida tanata zuzzubs tsumi a roba wanda ta zabga uban flavour a ciki seka ɗauka tsumin arziƙine bakinta ɗauke da sallama tashiga ba wanda ya amsamata Inteesar tayi gurin Innah Uwar Gwarama ta duƙa cikin ladabi tace"Innah sannu da hutawa".
taɓe baki Uwar Gwarama tayi tare da cigaba da zuba tsuminta ba tare dataji haushiba ta miƙe tafara tafiya bazato taji su Ruƙayya da Bilki sun tintsire da dariya Bilki tace"dolema mutum ya rasa mashinshini tunda an riga angama badakai a waje".
"kema dai banda abinki waye zeje ya auri ragowar ƙarti yanaji yana gani da kuɗinsa".
"wallahi sede a ƙare abinsu waje ba'ah wannan hotel ba'ah wancan yawon karuwanci da sunan makaranta".
wata matashiyar yarinya ce tafito me tsananin kama da Inteesar tace"badai yayata ke yawon karuwanciba sede waccan".
ta nuna Uwar Gwarama dake zuzzuba tsumi nanfa Uwar Gwarama tashiga bala'i tana cewa"ƙarya akemata ai gaskiya suka faɗa inbanda ta tsaya yawon barikinta aida tini tasamu miji saboda kowa yasan metake aikatawa mijin aurema ya gagareta ba'ah taɓa zuwa nan gidan da koda sau ɗayane gurin Inteesar ba".
"hakane Iyah muma nan gida zamu barta danba mesonta".
suna cikin wannan maganar Abbansu ya shigo fashewa Uwar Gwarama tayi da kuka tashiga zayyanemasa ƙarya da gaskiya aiko yashiga jibgar Inteesar da Khadija seda yayi me isarshi sannan ya kyalesu.

AFTER ONE DAY

Sanye Abbah yike da Uniform ɗin masu shara sega wani me irin kayansa gaisawa sukayi yace"a'ah Ahmadu se yanzu kazo".
"a'ah na daɗe da zuwa ina bayane yanzu gashi inji Oga tin ɗazu yabayar yace abaka inkazo".

ansa Abbah yayi yana dubawa yaga takardar sallamace  daga aikice sosai hankalinshi ya tashi yana ƙoƙarin tafiya office ɗin Ahmad Malam Ahmadu ya dakatar dashi tare da cewa"yace kar abarka ka shiga gurinsa".
sosai hankalin Abbah yaƙara tashi a wannan ranar duk yadda yaso dayaga Ahmad abu ya faskara dole haka ya tafi gida.

Jiki ba kwari haka Abbah yashiga gida tare da zama kusa da Uwar Gwarama jiki a sanyaye kallonshi Uwar Gwarama tayi tare da cewa"lafiya kashigo hannu na dukan cinya Malam".
"Ladidi an koreni a aiki".
Khadijat dake zagayowa dake zagayowa daka backyard ɗin gidan ce wani farinciki duk ya lulluɓeta da murnarta ta shiga ɗakinsu tana ƴan waƙe-waƙenta ɗago kai Inteesar tayi daga karatun Alqur'anin da takeyi tare da cewa"meyafaru naga kina murna".
"Abbah aka kora a gurin aikinsu".
"shine kuma kike murna".
"eyi ai gwarama da aka koresa daga aikin koba komai a dena banbantamu da ƴaƴan so  shima yaji yadda mukeji a zuciyarmu  na abinda yikemana kamar ba ƴaƴansa ba duk ya tsanemu ni wani lokacin har tinani nike anyako Abbah ne babanmu".
"Khadija meyasa kike irin wannan ne koba komai ai mahaifinmune kidena irin wannan inkuma ba hakaba zamu ɓata".
"yi haƙuri Aunty".!!!!!!

Votes and Comments
Plz share fisabilillah

*Dan Allah a tayani share*

_*Daga Alƙalamun ƴar Mutanen Gwarzo.*_
🌻 *THE WORLD MAN*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK  1*

*PAGES*0️⃣3️⃣➡️0️⃣4️⃣

Jiki ba kwari Abbah yamiƙe yaɗauki buta ya zagaya be wani jimaba segashi yafito yaƙara zama kusa da Uwar Gwarama baki buɗe Uwar Gwarama ke kallon Abbah sannan tace"amma dai gaskiya Malam se yanzu na yarda da zancen Uwani na cewa zuciyarka a mace take murus yo inbanda haka meyasa bazaka nace gurin wannan yaro arziƙinba kaji ba'asin abinda yasa ya korekaba se kawai ka yayo jiki ka tawo gida to wlh Malam ahir ɗinka dan tashi zakayi ka koma bazan riƙa ci dakai da wata ƙatuwa da ƴaƴanta ba akan wanne dalilin kamar kai nikeyiwa neman imma zaka tashi kaje kaji meke faruwa kaje danni bama zan iya cida me ƙashin tsiyaba wallahi wani yahana uwarsu yin sana'ah tace se ƴaƴanta sunyi karatun boko yanzu aisaci boko a wuta aikaga ko maga abinda bokon nasu ze tsinanamasu dukda bamma yadda bokon akeyiba ba babban bokoba wanda harka mutu baza'ah dena yimaka gori ba danni bame ɓatani ƴaƴana basu jawomun abun kunyaba na wata su jawomun haka kurum a'ah ba dani za'ayi wannan sa lallen kazarba atoh".
har Uwar Gwarama ta gama zazzage Abbah becemata ƙalaba yashafa sumar kansa tare da cewa"to a temakeni da abinci konaji sanyi a zuciyata".
wani banzan kallo da Uwar Gwarama ta makawa Abbah da sauri ya miƙe tare da washe baki yace"ya haƙuri bara inje ɗin".
"yadaifimaka ".
nan Abbah yafara tafiya daidai nan Wata matashiyar mata tayi sallama wadda bazata wuce shekaru42 ba jin Uwar Gwarama bata ansamata ba haka Abbah shima ta nufi ɗakinta.

Tana shiga Khadijana yiwa Inteesar kitso ta saki da sauri ta rungumeta tare da cewa"sannu da dawowa Ummah".
murmushi Umma tayi itama Inteesar ta rungumeta rungumesu tayi gabaki ɗayansu sannan tace"ko ni Aishatu zaku karyani ku sakeni inzauna".
murmushi sukayi gabaki ɗayansu suka zauna cikin farinciki Inteesar tace"ya aka baro su Halima".
"suna gaidaku".
cikin zumuɗi Khadija tace"Ummah kinsan wani abun farin ciki ko daya samemu kuwa".
cikin farim ciki Ummah tace"Auta meya samemu haka naga kina farin ciki haka".
kallonta Inteesar take da mamaki dan ita batasan meya samesu na farinciki da Khadija keta farin ciki hakaba tana wannan tinanin ta tsinkayi muryar Khadija na cewa"Ummah anfa kori Abbah daka gurin aikinsa kinji daɗin danaji kuwa ".
haɗe rai Ummah tayi tare da cewa"Khadija meke damunki ne haka da har kike farinciki dan an kori mahaifinki daga aiki ashe duk huɗubar danakemuku ke bata shiga kunnenki Khadija mahaifinku nefa kome yike yimana bekamata kiyi farin cikiba Khadija ".
"ai Ummah……".
saurin katseta Ummah tayi ta hanyar cewa"ya isheki haka a rayuwa duk wanda bashi da haƙuri baze kai labari ba kuma komai na duniya ɗan haƙurine watarana se labari komai kaga yasamu bawa da sanin Allah kuma komai muƙaddarine daga Allah ba'ah taɓa dawwama a abu ɗaya shiyasa kullum bani da abinda zancemuku sede kuyi haƙuri kunji shi haƙuri riba garesa".

Ummah na cikin yimusu magana Uwar Gwarama ta buɗe ƙofa cikin masifa tace"ga kayana can kije ki wanken".
ta wuce fuu Ummah takalli Inteesar tare da cewa"tashi kije kiyimata".
"toh".
zumɓurar baki Khadija tayi tare da cewa"saboda Allah Ummah duk gasu Bilki da Ruƙayya bazasuyiba se Aunty saboda itace karkatacciyar kukar gidannan me daɗin hawa haba".
"au bakiji nasihar dana gama yumuku ba kenan ko saboda kinada kunnen ƙashi ko".
Inteesar ta fita tsakar gida Khadija ma tabita tashiga tayata cikin kayan harda nasu Bilki da Ruƙayya hattana pant ɗinsu da suka gama period seda suka haɗa nan Inteesar tashiga wankemusu.

Kwance yike akan sofa ya lumshe idanunsa kamar me bacci a hankali ya buɗe idanunsa da suka yimasa nauyi yayi kana ganin fuskarsa zaka gane yanada damuwa tashi yayi ya nufi tanƙamemeb wardrobe ɗinsa ya buɗe ya zari wasu haɗaɗɗun ƴan kanti yasaka ya feshe jikinsa da turarukansa masu daɗi kanshi sannan ya ɗauki phones ɗinsa ya fita.

A hankali yike sakkowa daga stairs yana ɗaura gucci watch a hannunsa tunda ta ɗaura idanunta akansa ko ƙiftawa batayi harya ƙarasa sakkowa cikin takunsa kamar yana tausayin ƙasa yaƙarasa sauka ya nufi falon Haneefa ce zaune ita kaɗai cikin wasu english wears riga da wando rigar kusan rabin ƙirjinta a waje fuska tasha heavy make-up kamar ga atarch yare-yare da murmushi tace"morning sweetheart".
Abdallah(Namijin duniya) kallo ɗaya yayimata ya ɗauke kansa gefe yaƙara haɗe rai kamar wanda aka aikomasa da mutuwa yace"Ify what of you".
"lafiya ƙlau".
ya miƙe ya nufi ƙofa ɓangaren granny ɗinsa ya nufa yana shiga ya tadda Abbih ɗinsa da Mummy zaune ƙarasawa yayi bakinsa ɗauke da sallama ƙasa-ƙasa taɓe baki Innah tayi tare da cewa"yaudai ban dafa abincina dakaiba dunkum dangin tsaka atoh inma zakaci abinci da Mamanka tayi kaci dan bazan bakaba".
dariya Mummy tayi tare da cewa"rabu da ita Son ai se inbaka nawa".
murmushin gefan baki yayi ya zauna tare da cewa"ina kwananku ".
"lafiya ƙlau Son yaka tashi".
"lafiya ƙlau Abbih".
"masha Allah".
miƙewa Abbih yayi tare da cewa"Ammi ni zan wuce inada wani meeting".
"to Allah ya tsare".
"Ameen ya Allah Son seka fito".
"toh Abbih".
nanya fita Mummy ta miƙe tace"Ammi se anjima Son seka dawo ".
"toh"
yafaɗa a daƙile Mummy washe baki Ammi tayi tare da cewa"toh Fatimah Allah yayimiki albarka".

"Ameen".
nanta tafi murmushi Abdallah yayi ganin Ammi ta kauda kanta gefe yaƙarasa gurinta tare da cewa"Ammi an tashi lafiya".
"da ban kwanaba ka ganni zaune kamar duniya ne".
murmushi yayi yace"Ammi tuba nike ayi haƙuri".
"aini tunda kaƙi jin maganata nabarka da halinka ace yaro kamar wanda akayiwa mugun abu bakason yin aure anjuma nan zan shirya inje gidan aminiyata inma wani abun akayimaka naji dan bazan bari a cuci jikana kwalli ɗaya ba a duniya atoh bara in zubomaka abinci inshirya ku ajeni gidan Ta Annabi ina dalili ina ɗan mafari a sabautamun jikana ga abokinka har zeyi aure nanda sati biyu amma kai shiru akeji ".
bece komaiba a ta wuce a zuciyarsa yace"hmm Ammi bazaki gane abinda ke damuna ba a duniya ba macen da zata yarda ta aureni matsawar tasan meke damuna".
yana wannan zancen Ammi ta fito ta ajemasa plate ɗin irish kaɗan yaci ya miƙe tare da kallon agogon hannunsa yace"Ammi sena dawo bara se su Muhd su kaiki ni kuma na wuce inada meeting".
"toh seka dawo".
nanya fice ta taɓe baki tare da cewa"imma wanine yasamun hannu agun jikana zanji koma meye".
nanta tafi ɗaki ta shirya ta fita suka tafi.

Yana fita ya shiga mota suka fara tafiya har sun ɗauki hanyar gurin aikinsu ba tare daya buɗe idoba yace"Hospital zamu".
"toh Oga".
nan suka canza akalar motar suka nufi wani katafaren asibiti suna isa ya zagaya ya buɗemasa nanya fita cikin takunsa na isa harya isa ciki ya nufi office ɗin doctor Muhseen murya can ƙasa yayi sallama ya shiga murmushi ɗauke a fuskar doctor Muhseen yace"sannu da shigowa".
"yauwa".
Namijin duniya yafaɗa tare da zama kan kujerar dake kusa table ɗin Muhseen ya miƙamasa hannu suka gaisa bayan sun gaisa Doctor Muhseen ya ɗakko wata farar leda tare da miƙawa Namijin duniya ya ansa cikeda kulawa Doctor Muhseen yace"bara inɗakko maka water seka sha".
"ohk".
nanya ɗakko mishi ya buɗe drugs ya buɗe bottle yasha sannan ya miƙe yace"se anjuma".
nan ya fita be jira amsar doctor Muhseen ba wani irin tausayin Namijin duniya ne yakama doctor Muhseen a hankali ya furta "Allah na sane dakai Abdallah insha Allahu Allah ze baka lafiya kamar ko wanne mutum".
nanya nutsatsa yana tinanin Allah yabawa Namijin duniya komai amma Allah ya rageshi da wata babbar ƙaddara megirma yace"insha Allahu Abdallah zaka cinye wannan jarabawar".
jiki a sanyaye ya cigaba da cike files ɗin dake gabansa.

5:00pm

Zaune Abdallah yike yana  danna phone ɗinsa  kallo ɗaya zakayimasa kasan tinani kawai yikeyi a guest house ɗinsa Ahmad ya buɗe ƙofar falo har ya ƙaraso inda yike Namijin duniya kasan cewa yayi zurfi a cikin tinani domin ko sallamar da Ahmad yayi be amsaba taɓashi Ahmad yayi da sauri ya ɗago ya kalli Ahmad dafashi Ahmad yayi tare da cewa"Abdallah meyasa koda yaushe kakeson ɓoyemana damuwarka ne tin muna yara baka da abokan da suka fimu inbaka faɗamana damuwarkaba wazaka faɗawa".
sauke numfashi Namijin duniya yayi tare da cewa"bakomai Ahmad inda dashi dana faɗamaka".
"ohk to meyasa kasa na kori mutum haka kurum ba dalili dafa wannan aikin sukecin abincifa shida iyalansa".
sauke numfashi Namijin duniya yayi  tare da labartawa Ahmad komai da Inteesar  tayi masa murmushi Ahmad yayi  tare da cewa "haba My Man  aiba haka yakamata kayiba ai kan yarinyar yakamata ka huce ".
kallonsa namijin duniya yayi alamun yana san sanin mezaiyi mata murmushi Ahmad yayi tare dakai bakinsa saitin  kunnensa yayimasa  raɗa wata magana wadda nima kaina Real eeshow bansan meya faɗamasa ba lokaci ɗaya namijin duniya yasaki wani murmushin gefan baki tare da furta "amma Ahmad kana ganin ba raini a wannan shawarar taka kuwa ?".
"wanne irin raini My Man ai wannance kawai hanyar da zaka  rama kenan  a ganina".
shiru Namijin duniya yayi kafin daga bisani ya saki wani ƙayataccen murmushi saboda se yanzu yagane abinda Ahmad yike nufi  cikin jindaɗin shawarar Ahmad ya furta "shiyasa nike ƙara ƙaunarka saboda kai akwai kawo light".
 dariya su dukansu sukayi sai a sannan namijin duniya yaɗanji ranshi yayi sanyi nan suka koma hirar bikin Adam  daga bisani Ahmad ya ɗaga waya yayi sai kuma ya aje naga yayi murmushi Babu ɓata lokaci sakataren Ahmad yashigo shida wani ɗan dattijon mutum abayansa.

 Zama sukayi a ƙasan carpet  cikin girnamawa sakataren Ahmad yace"ranka yadaɗe gashinan".
"ohk we can go".
 nan yafice  yabarsu da Abbah daketa ƴan kalle-kalle saboda  tinda yike bai taɓa ganin tsararren guri ba kamar wannanba saboda falon yagaji da haɗuwa komai na more rayuwa akwaisa a falon   gefe guda kuma tanƙama-tanƙaman photunan Namijin duniyane a kowanne bango na falon
 dakyar ya ɗauke idanunsa daga kalle kalle yamaida ƙasa cikin rawar jiki ya  gaishesu  Ahmad ne kawai  ya amsa namijin duniya kuwa kallo ɗaya yayi masa yakauda kai ya taɓe baki a zuciyarsa yace"dama wannan ne mahaifin dirty girl ɗinnan  yarinyar nan mara tarbiyya dubeshi wani iri".
yana cikin wannan zancen zucin yaji Ahmad yace "dama abinda yasa kaga
 na sallameka agurin aiki babu laifin dakayi  dama wata sabuwar dokace tafito mun dena ɗaukar tsofaffi da wa'inda basuda kwalin degree amma idan kana da wanda zaka kawo mai kwalin degree tom ka kawo sai yamaye gurbinka ko mace ko namiji  amma bada Comphany ɗina za ai aikiba na Namijin duniya ne zasu ɗaukesa".

Cikin farin ciki yaɗago ya kallesa yana washe baki  Abbah yayi tare da cewa"to ranka yadaɗe Allah yasaka da alkhairi nagode Allah yaƙara arziƙi amma banida wani namiji dayayi wannan karatun sai dai mace zan iya kawota?"
Murmushi Ahmad yayi tare da cewa "ai babu komai Baba kakawota inhar tana da degree".
shiru Abbah yayi daga bisani yace"ammafa wani hanzari ba guduba ita da ƙawarta suke komai Alhaji Zannah ne yayiwa yarinyar tawa komai be kamata na samarwa tawaba itakuma tashi nayi musu hakaba koba komai be taɓa ware tawaba  abawa  tashin kawai se a kyale Inteesar ɗin".
damm ƙirjin Namijin duniya yabayar daketa shan ƙanshi  jiyayi kamar yasamusu baki amma saboda tsabar girman kai da izza bazaka gane yaji wani abuba yacigaba da  operating ɗin phone ɗinsa  jiyayi Ahmad yace"a'ah Babah ka kawosu kawai gabaki ɗayansu a kawosu  sesuyi interview in Allah yakaimu gobe".
Wani farincikine ya lulluɓe Abbah nan yadungi zabga godiya yatafi yana tafe yana murna ganin aikinsa yadawo bai suɓucemasa ba.

Murmushi namijin duniya yayi wanda shikaɗai yasan ma'anarsa yabawa Ahmad hannu suka kashe Ahmad yace"to tazo hannu saura plan ɗinmu na biyu ita harta isa taja da ɗaya daga cikin ɗan cliff ɗinmu Tripple A saura shawarar Adam shima aji tabakinsa daganan semuyi tsare-tsaren biki".
"toh tashi muje".
nansuka  tafi yayinda ran Namijin duniya yayi fess ji  yike kamar yajawo gobe tayi.

Washe gari tin safe Namijin duniya ya shirya ko breakfast be tsaya yayiba  yafito yana ɗaura agogon rolex a hannunsa yaga Abbih ɗinsa zaune a dining gefensa Mummy zaune ƙarasawa yayi gurin Abbih ɗinsa yayin ɗinsa sannan yace"Abbihna ka tashi lafiya".
"lafiya ƙlau Babana harka sakko da wuri haka".
"eh sauri nike zanyi wani abu".
"okay yanaga yau kana cikin farincikiko ko suruka aka yimun".
wani smiling Namijin duniya yayi wanda ko Abbih ɗinsa rabon dayaga yayisa harya manta  yaji yace"Abbih the weather is so nice today".
murmushi Abbih yayi nanya gaida Mummy data tsaya kallonsu sannan yayimusu sallama yafita ba tare  dayaci komaiba.

Yana isa ya wuce Office ɗinsa  direct koda yashiga yaja kujera yazauna  tare da lumshe ido yayi shiru yashiga dunuyar tinani jiyayi anbuɗe ƙofa
sakatariya ce tashigo sai faman karai-raye karai-raye take da jiki dukda ƙamas take ga shegun riga da wando data saka  sun matseta rabin breast ɗinta da suka zube kamar silifas a waje tasha heavy  makeup sai taunar cingam take kamar karuwa baki ta saki ganinsa zaune akan kujera har yazo  gani tayi shikaɗai se murmushin gefan baki yake lokaci ɗaya taƙara cigaba da

karairayarta dan ita a tinaninta ita yikeyiwa taƙarasa gabanshu cikin yauƙi da iyayi irin na ƴan bariki tace"yallabai
barka da hut meza'ah kawo maka bayan coffee".
taƙaraasa zancenta tana ƙuresa da kallo
Gyara zamansa yayi ba tare daya kalleta ba a daƙile yace"yau bana buƙatar komai".
yafaɗa sai kallonta yaƙarasa zancensa tare da ƙara sakin wani murmushin
Ganin yanamata murmushi ne saitaga kamar da ita yake tako ƙara gyara gaban rigarta tana tsaida shafaffun nonuwanta wa'inda suka kwanta kamar lawashin albasa tana tunkarosa gani yayi tana matsowa gabdashi dan-danan yatattaro ɓacin rai yaɗorawa fuskarsa yahaɗe rai murtuke kamar bashine yagama murmushi yanzuba tana ganin haka tayi saurin wayencewa taƙarasa cikin freidge taɗauko cups tatafi dasu zata wanke tana fita taja dogon numfashi "yau danayi gisgirin taɓa oga dana shiga uku ashe murmushin danaga yanayi badani yakeba to dawa yike danni dai bazan taɓa bari Oga ya airi wataba koda zan rasa zanin ɗaurawa wallahi dole inƙara zuwa gurin boka na bayan tsauni yayimun maganinshi yau naso na gwadamasa irin tawa soyayyar".
take faɗa aranta nanta wuce tazauna tana maida numfashi ta ɗauki wayarta tashiga dialing number ƙawarta bugu ɗaya ta ɗauka tare da cewa!!!!!

*Idan naga ruwan comments da votes zakuga cigaban kullum ta Allah har sau biyu a rana idan ban ganiba daka wannan na dena wannan book ɗin.*

Votes and Comments
Plz share sisters and brothers to others fisabilillah

_*Daga Alƙalamun ƴa🌻 *THE WORLD MAN*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK 1*

*PAGES*05➡️0️⃣6️⃣

"Lafiya irin wannan kira haka da sassafiyar nan kota warune".

"hmm ai dole na kiraki hankalina ne Zuby yayi mugun tashi".
"faɗamun mana Feenah".
"yau ina zuwa na tadda Oga harya zo yanata murmushi da farko na zata dani yike Allah yasoni da harnaje in rungumesa nayi saurin wayancewa saboda kingako yadda ya haɗe rai lokaci ɗaya da tini nasamu matsala bakiji yadda naji ba saboda tsoro nike Allah yasa dai ba wata ya haɗu da itaba dan wallahi Zuby bazan taɓa jurar ganin Abdallah da wata ba ko zan rasa zanin ɗaurawa sena nisantashi da mata matsawar bani ze aura ba".
"kece Feenah tin yaushe nike cemiki koda muna yin amfani da maganin Bokanan to dole kema ki riƙa nunamasa kefa kina sonsa akwai wasu kaya danaga Hajiya Riga ta ɗakko ƴan gumamane masu kyau anjuma kizo muje gidan ki zaɓa zakisha mamakin yadda ze riƙa kallonki kamar wani magnet haka ze riƙa binki da ido saboda zasusa sha'awarsa ta motsa kinga dakanan kekuma sekisan yadda zakiyi har yayi  sex dake dakanan zamu kamashi a hannu ta hanyar cemasa kinada ciki kamar yadda yike popular once bazeso ace zamu tonamasa asiriba duniya tasani  kinga semuyi amfani da wannan damar muce masa sede ya aureki inba hakaba mu tona masa asiri".
"wow gaskiya ƙawata kinyi dogon tinani  sosai yanzu zan cigaba da nunamasa inasonsa dukda nasan ya gane   hmmm inyazo hannu ze gane kurensa dan yadda yabamu wahala semun fanshe".
"ai dole yagane kurensa Allah yasa karki samu duniya ki manta dani danke ɗan tsakoce samu kaƙi dangi   kina samun abun duniya zaki yimun ƴan ta waye".
"haba Zuby aina dena yimiki haka  ai anzama ɗaya tare dake zamuci duniyarmu a tsinke ko banza a riƙa nunomu a mujallu".
"toh ƙawata bara na tashi tunda kin tasheni ".
"toh dan Allah da kinjemun gurin bokan danni banga alamun aikinnan yanayiba  ƙinji ta bakinsa".
"aiko kema kince wani abu bara  na shirya senaje gurin wani Bokan danaga su Mum ɗina suna zuwa aikinsa kamar yankan wuƙa haka yike ammafa  sekin kawo wani abu".
"kema dai ƙawata kinsan da wannan Bokan kikasa mukaita kashe kuɗi gurin wannan da aikinsa bayayi bara inyimiki transfer kiyi sauri dan Allah".
"toh aikeɗince ƙawata bakya sakin kuɗi sosai tayayako zankaiki gurin wannan  da manyan mutane ke zuwa shiyasama ban sanar dakeba".
"kinsan dai ko nawane zan iya kashewa matsawar Namijin duniya ze aureni a riƙa kirana ta Mrs Namijin duniya ai zan bada ko nawane yanzu bara nafara turamiki idan bazasu isaba ki kirani".
"toh ina jiranki dan inyi maza indawo".
"toh".
nansukayi sallama ta  gyara zamanta ta cigaba da haɗa files ɗin da zata shigarwa da Namijin duniya.

Ɓangaren Zuby ko tana kashe waya ta tintsire da dariya mahaifiyarta dake kusa da itace ta kalleta alamun dariyar metake tsagaitawa da dariya Zuby tayi tare da cewa"yanzu karyar zata turon da kuɗi Mum semuje gurin bokannan da kikeso muje ita inbanda itama tinkiyace ta ina zan bari inaji ina gani ta auri Namijin duniya bayan nina fara nunamata shi a rayuwarta tasameni ina sakatariyata tasa aka koreni a tinaninta kyaleta zanyi to wallahi yanzune ko

zatasan wutsiyar raƙumi tayi nisa da ƙasa zan nunamata na rigata zuwa duniya koya kikace Mum".
washe baki Mum tayi tare da cewa"aiko yanzu zanzo inkira Hajiya Mansura ta shirya muje ayimiki aikinnan dama kuɗine sukai tsaiko to yanzu Allah ya kawo na banza bara naje na wanki bayan tukunya a ɗaura a leda seki kaimata a matsayin maganin sede taga anayi Namijin duniya mijinkine ke kaɗai Zubyna".
"yauwa Mum".
nan Mum takira Hajiya Mansura tasanarmata suka cigaba da harkokinsu.

Zaune take akan kujera tana wanke-wanke Khadijat na ɗaurayemata Abbah yashigo fangan-fangan ya wuce ɗakin Uwar Gwarama zaune yasameta tana ƙullin magungunan mata zama yayi kusa da ita tare da cewa"yaufa yakamata suje yarannan shine nace bara insanarmiki".
"toh kayimata magana ammafa albashin gabaki ɗaya namune kasansu da baƙin hali kar wani lokacin ace sun faɗi".
"toh".
nanya fita kallo ɗaya yayimusu ya kauda kai  tare da cewa"kee".
cikin ɓarin jiki Inteesar ta miƙe dantasan da ita Abbah yike cikin ladabi taƙarasa inda yike ta duƙa tare da cewa"gani Abbah".
"ki shirya yanzu kutafi keda Hauwa kuje ma'aikatar Namijin duniya zakuyi interview yike kome saura kuma ki nuna baƙin halin naki a canma".
 gaban Inteesar ne yayi mummanan faɗuwa jin sunan da Abbah yafaɗa dakyar ta saita nutsuwarta cikin sanyin jiki tace"toh Abbah angode Allah yasaka da alkhairi".
jin muryar Uwar Gwarama tayi akanta tace"bar wani saurin godiya munafuka Malam baka faɗamata ni za'ah riƙa kawowa kuɗin bane".
taƙarasa zancenta tare da jifan Abbah da wani banzan kallon daya hautsinamasa ƴan hanji cikin rawar murya yace "ayi haƙuri ai bankai ga sanar da ita bane".
"ka gama munafuncinka".
suna wannan zancen wata mata tashigo tashigo gidan da sauri Uwar Gwarama na ganinta tace"Hassatu  badai Jummalar bace kikaga ta wuceba".
"ita ce kuwa yanzunnan tashiga gidanta".
"to bara naje yau koni ko ita wallahi".
nanta wuce ta tafi tana isa gidan Jummala sukayi kaciɓus a zaure zata fita saurin riƙota Uwar Gwarama tayi cikin masifa tace"wallahi sekin bani kuɗina ina dalili ina ɗan mafari tunkan inhau ruwan cikinki ki bani kuɗina".
"kiyi haƙuri idan nasamu zan aikomiki dasu inzo inyimiki godiya".
"wuce muje cikin gidan kome kike dashi kibani na daidai kuɗina".
nanta tasa ƙeyar Jummai suka shiga ta buɗemata ƙofa ganin akwati uku a ɗakin yasa Uwar Gwarama ta ɗauka tare da cewa"naɗauki wa'innan dukda nasan kuɗina basukai wannanba dama akwai ɗan tala dayace inhaɗamasa akwati zeyi aure idan na haɗamishi se inbaki sauran canjinki".
zaro ido Jummai tayi tace"ki rufamun asiri  Uwar Gwarama kayan Nura ne ya siyo ze fara haɗa lefe".

"ko kayan waye naɗauka ɗin".
nanta ɗauka ta tafi abinta.

Tin fitowarsu Inteesar taga yanayin Hauwa'uh kamar mara lafiya gashi tayi shiru cikin kulawa Inteesar tace"Hauwa'uh lafiyarki kuwa naga duk jikinki yayi sanyi kamar wadda wani abun ke damunta".
"hmm Inteesar tinani nikeyi saboda Comphany ɗin da zamufa na Namijin duniya ne bakya tinanin idan yaganmufa inajin tsoron abinda zemikine".
tsaki Inteesar tayi saboda ita harta manta da abinda yafaru tsakaninsu tace"hmm halinki yana bani mamaki Hauwa'uh mufa sukayiwa laifi ba mumuka musuba bana taɓa regreting ɗin abinda nayimasa kuma ko yanzu yakuma yimana wani abun wallahi sena rama be isa yayimana abinda Allah bemana ba irin kune marasa kishin kansu da se a takasu su kyale".
suna wannan zancen suka ƙaraso titi suka tsaya jiran napep basu daɗe da tsayuwaba suka samu adaidaita suka hau suka tafi.

Suna sauka Inteesar taji gabanta yayi mummunan faɗuwa dakyar ta tattaro sauran nutsuwar data ragemata da jarumta ta dake suka shiga inda akeyiwa mutane interview suka zauna.

Namijin duniya dake zaune a Office ɗinsa yana ganinsu Inteesar ne yasaki wani ƙasaitaccen murmushi me cike da ma'anoni kala-kala yace"yarinya kin shigo hannu zakisan wanene Namijin duniya zaki tantwncemun waye me ƙazamun hannu cikin ni dake waye mara tarbiyya cikin ni dake".
ya miƙe yafita bin bayansa sakatariya tayi tana tinanin ina Ogan nata zeje gani tayi sunyi hanyar inda akeyiwa mutane interview mamakine yakamata tasan ogannata baya zuwa irin wa'innan guraren bata ƙara tsinkewa da al'amarinba seda taga Ahmad da Adam suma tsaye bayansu da sakatariyansu suma tana wannan mamakin har suka ƙarasa inda su Adam suke cikin girmamawa aka shiga gaida Namijin duniya cikin takun isa suka jera Tripple Apple suka jera kallo ɗaya Namijin duniya yayiwa su Inteesar ya ɗauke kai kamar be gansuba sunzo dafda su Inteesar ganin mutane hadda tsofaffi nata duƙawa har ƙasa suna gaidasu kamar zasuyi sujjada sukuma sun wani ɗauke kai ko amsawa basayi hakan baƙaramun ɓata ran Inteesar yayiba taja tsaki karaf a kunnen Namijin duniya dake side ɗinta suna haɗa ido ta taɓe baki cikin ƙasa da murya tace"mara tarbiyya kawai da rashin sanin darajar ɗan adam".
baƙaramun ɓaci ran Namijin duniya yaƙara yi da Inteesar ba be nuna yaji komaiba har suka shiga theater da za'ah fara interview ɗin suka zauna lokaci ɗaya idanunsa dake cikin baƙin glass suka canza kala fuskarnan taƙara haɗewa kamar hadarin kaka aka fara kiran mutane suna shigowa.

Se yamma liƙis sannan akayi kiran sunan Hauwa'uh aka kira na Inteesar a tare suka shiga theater suna shiga sun zauna kenan su Namijin duniya suka miƙe cikin gadara Ahmad yace"muntashi gobe kuzo da wuri ayimuku Muh'd ɗauki sunansu gobe dasu zamu fara".
"toh ranka shidaɗe".
nansuka wuce suka barsu nan sosai ran Inteesar ya ɓaci domin wa'inda sukazo bayan-bayansuma ammusu amma su saboda rainin hankali sukacemusu sun tashi Hauwa'uh

ce ta faɗawa Muh'd sunansu sannan suka tafi rai ɓace.

Zaune suke a falo suna hirarsu Ahmad yace"My Man kadena damun kanka kan wannan Babe ɗin  domin tarigada ta shigo hannu yanzu zata gane kurenta".
buɗe idonsa yayi yasaki murmushin gefan baki a zuciyarsa yace"zan koyamiki hankalin da har abada bazaki sake yiwa wani makamancin abinda kikayimunba ".
dariya Adam yayi tare da cewa"akan wannan Babe ɗin nafara ganin Namijin duniya yafara tinani dolene muyi maganinta ta yadda sunansa taji  seta suma".
"wallahi kuwa ai yanzu zata fara gane kurenta".
nansukaita hirarsu Namijin duniya ya miƙe ya nufi pridge yaɗauki bottle water yashiga bedroom yana zuwa yazauna gefan haɗaɗen italian bed ɗinsa yasa hannu yajawo loka dake kusa sa gadon yaɗauki ledar drugs ɗinsa yazauna sannan ya ɓaɓɓala yasha ya mayar loka ya kwanta tare da lumshe ido yashiga tinanin  wani mugun tausayin kansa  ne yakamasa lokaci ɗaya wasu hawaye masu zafi suka silalomasa yasa hanky ɗinsa ya share yanajin wani irin nauyi a zuciyarsa idan ya tino da irin ƙaddarar dake tare dashi tashi yayi yashiga toilet ɗinsa ya ɗauro alwala yashiga yin nafila yana kaiwa Allah kukansa kan Allah ya yayemasa lalurar dake damunsa.

Washe gari tin bakwai su Inteesar sukaje Comphany ɗin Namijin duniya amma har yamma ba'ah yimusuba sedaka baya sannan aka yiwa Hauwa'uh Inteesar na shiga suka miƙe   Adam ya kalleta tare da cewa"Madam muntashi sede gobe ki dawo da wuri".
ko kallonshi Inteesar batayiba cikin ɓacin rai tace"Hauwa'uh mutafi".
"toh mungode ranka shidaɗe".
Hauwa'uh batayi aune ba se ganin Inteesar tayi fuuu tayi waje kamar zata tashi sama kallon-kallon suka shigayi Ahmad yace"saura step two da alama wannan ya amsu".
"amma Ahmad baka ganin a zuciya irin ta wannan yarinyar zata iya ƙin zuwa gobe".
"hmm bazataƙi zuwaba saboda ninacemaka wannan Adam saboda da wannan aikin zasu dogara kagako dolenta tazo".
"hakane amma wannan mugune yasan kan tsiyar ".
namijin duniya dai becemusu komaiba nan suka tafi.

A bakin titi Hauwa'uh tasamu Inteesar tsaye murmushi Hauwa'uh tayi ganin Inteesar ta haɗe girar sama data ƙasa dafata tayi kaɓar da hannun Hauwa'uh Inteesar tayi tare da cewa"bazan ƙara zuwa ba Allah haka kurum inzo inda za'ah yita wulaƙantani Allah be wulaƙantaniba se wani banza can wanda tarbiyyama cikakka bashi da ita".
"haba Inteesar kinsan dai dole kije inbaso kike Abbah yayimiki wani abunba kowa da kika gani yanada zuwa a irin wannan abun se kanayi kana kai zuciya nesa sannan zaka samu abinda kake nema meya tsakanin yauda gobe goben muzo indai baso kike kijama Ummah abun tsiyaba".
"toh zanyi tinani akai danni bazan juri wulaƙanci wannan mara tarbiyyarba".
suna cikin hirarsu suka samu adaidaita suka hau suka nufi sileja.

Suna sauka sukaima juna sallama Inteesar nashiga soronsu taci karo da Bilki tana zance tazo

daidai wucesu tasaki tsaki tare da hararta tace"haka za'ah ƙare kullum cikin yawon bariki ba'ah can ba'ah nan anrasa mashunshini dole a riƙayimana ƴan gicce-gicce to ahir ɗinki Bashir yafi ƙarfinki".
murmushi kawai Inteesar tayi tare da yɗauke kanta tayi kamar bada ita takeba ta wuce abinta koda tashiga ɗakinsu ta labartawa Ummansu komai ta nunamata tayi haƙuri taje goben da sukacemata bata wani jima da zamaba tashiga aikin gida ba ita ta gama ba se tara na dare taje tayi wanka sannan Uwar Gwarama taɗan zubomusu abinci kaɗan  kamar yadda takeyi suka ansa sukaɗan lasa suka kwanta.

Washe garima da wuri suka nufi Comphany ɗin Namijin duniya shiga sukayi nan suka nufi hall ɗin da ake interview suna zuwa saka tadda bakowa sun juya kenan sukaga Sakatariya tana kallonsu a yatsine kamar wadda taga kashi tace"a cikinku wacece Inteesar".
"gani".
kallon tara saura kwata tayiwa Inteesar a zuciyarta tace"kome wannan ɗiyar talakawan zatayi a office ɗin Oga oho".
a fili kuma tace"kizo muje office ɗin Oga".
damm gaban Inteesar yabada lokaci ɗaya gumi yafara ketomata dakyar ta saita nutsuwarta tace"muje".
nan sakatariya tayi gaba tabarsu nan kallonta Hauwa'uh tayi tare da cewa"muje naga kin tsaya".
cikin dauriya ta aro jarumta dankarta lura tace"tom".
nansuka bi bayan sakatariya har suka isa bakin katafaren office ɗinsa kallonta Feenah tayi cikin yatsuna tace"kishiga".
"toh muje Hauwa'uh".
"a'ah Inteesar kawai yace ke kijirata anan ita tashiga".
lokaci ɗaya gaban Inteesar ya yanke tafaɗi komai nata seda ya tsaya cak saboda tinanin haɗuwarta da Namijin duniya jitayi kamar ta kwasa da gudu  a zuciyarta tace"nashiga uku Allah yasa  ba wani abun ya shiryamun ba saboda me za'ah ce ni kaɗai inshiga office ɗinsa anya bada wani abun a ƙasaba kuwa ni Inteesar".
wata zuciyar ce tace"kiyi addu'ah insha Allahu ba wani abunda ze faru se alkhairi kumama aiga Hauwa taga shigar office ɗin nasa ko wani abunne ya faru zata bada sheda".
 cikin ƙarfin hali tace"sena fito Hauwa'uh".
"tom Allah yabada sa'ah ".
"Ameen".
nanta danna wani switch ƙofa ta wangale  cikin sauri zuciyarta tashiga bugawa da ƙarfi gefe guda kuma tsoronsa ya dirarmata kanta a ƙasa tashiga tafiya!!!!!!!

*Yanzu naji duka naga ruwan comments naji daɗi nagode Allah uabarmu tare much love.*

Votes and comments
Plz share to others fisabilillah

_*Daga  Alƙalamun ƴar Mutanen Gwarzo.*_r Mutanen Gwarzo.*_
🌻 *MAN OF THE WORLD*

(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK  1*

*PAGES*0️⃣7️⃣➡️0️⃣8️⃣

Dukda kanta na ƙasa hakan be hana ƙamshin daddaɗan turarensa ya bugi hancinta ba lokaci ɗaya ta lumshe luli eyes ɗinta ta buɗesu akan tanƙamemen office ɗin Namijin duniya daya gaji da haɗuwa da abubuwan more rayuwa juyawar nan da zatayi tayi ido huɗu da wani tanƙamemen photon Namijin duniya yasha black suit a zaune ya ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya sumar nan kamar kullum a kwance tayi luff da ita lokaci ɗaya taji wata mummunar faɗuwar gaba wadda bata taɓa jintaba a hankali tashiga bin ko ina na office ɗin da kallo juyawar nan da zatayi taci karo da Namijin duniya harɗe kan kujerar office tana juyashi karaf idanunsu yafaɗa na juna da sauri Inteesar tayi ƙasa da kanta ƙirjinta na dukan tara-tara a haka harta isa gaban Namijin duniya da yike ƴan rubuce-rubucensa bazato taji yace"saboda tsabar rashin tarbiyya sallamarma baki iyaba".
dukda tasan bata da gaskiya amma hakan besata ta nunamasa ba sema ƙara haɗe rai datayi a ciki-ciki tace"Salamu Alaikum".
ba tare daya ɗago ba kamar ammasa dole yace"wa'alaki salam".
"ina yini".
wani banzan kallo me cike da tsana yake cifanta dashi ganin haka yasa Inteesar ta ƙara shan kunu ta tsuke ɗan pinky lips ɗinta niyyar zama takeyi akan ɗaya daka cikin kujerun dake gaban table ɗinsa ba zato taji ya bugamata tsawa cikin gadara da nuna isa yace"karki haumin kujera da wannan ƙazamin jikin naki da ba lallaima kina wankaba mara tsarki chairs ɗina na zaman masu tsarkine bana zaman faƙirai irinki ba".
tsam Inteesar ta matsa tare da makamasa wata banzar harara cikin ɓacin rai tace"banzo nan gurin  danka wulaƙani ba dan haka Malam dakata ka iya bakinka danni ba sakarkarun matannan bace wadda abin duniya ze rifemusu ido ayita yimusu wulaƙanci sunaji suna gani saboda abun duniya me kake dashi me gareka kaifa mutum ne kamar kowa balle intsaya kayita rainamun hankali inaji ina gani".
cikin muryarsa me nuni daya kai ƙololuwar ɓacin rai yace"kinsan ko dawa kike magana kuwa".

Kallonsa Inteesar tayi daga sama har ƙasa tace"eyi nasan da wanda nike magana man mara sanin darajar ɗan adam wanda baida tarbiyya ko kaɗan a gari nike magana man".
cikin zafin nama yana huci kamar wani mayunwacin zaki yayi kanta lokaci ɗaya ganin yadda yanayinsa ya canza yasa wani masifaffen tsoronsa ya dirarwa Inteesae tashiga yin baya yana binta harta ƙure da bango ya ɗaga hannu da niyyar yarfamata saboda firgici hakan yasata rife oily eyes ɗinta lokaci ɗaya eye lashes ɗinta suka sauka bazar tsintar kansa yayi da ƙin marinta

sema kallonta daya shigayi jin bataji saukar mari ba ne yasa Inteesar buɗe  kyawawan eye balls ɗinta ta saukesu akan Namijin duniya bazato taji hannunsa a saman waist ɗinta ya matseta da jikinsa cikin ɗaga murya yace"cikin ni dake yau za'ah ga me tarbiyya dan yau sena nunamiki bani da tarbiyya badai ni kike kira mara tarbiyya ba zan gwadamiki rashin tarbiyya".
ta buɗe baki da niyyar yimasa magana kenan bazato taji bakinsa cikin nata dukda irin tutturesa da take hakan besa ya kyaleta ba seda ya tsutsi bakinta kamar ba gobe jin alamu za'ah shigone yasashi saurin sakin Inteesar daketa hawaye yakoma ya zauna sosai take kuka harda shashsheƙa zatayi magana kenan Sakatariya Feenah tashigo suna haɗa  ido da Inteesar Feenah ta makamata wata uwar harara cikin takun ƴan bariki da ko ina na jikinta yana motsi tana niyyar ƙarasawa inda namijin duniya ke zaune bazato taji muryarshi cikin ɓacin rai yace"waya kirawoki da kawai zaki faɗowa mutane Office ba knocking".
batare data nuna taji haushi ba sema zaman rigar jikinta data shiga gyarawa  tayi dan silifas ɗin ƙirjinta yaƙara fitowa tace"sorry sir dama nashigone dan intambayeka ko kana buƙatar wani abunne".
"dama in inada buƙatar wani abun ba danna switch nike ba".
"sorry sir".
tafaɗa cikin girmamawa  ta juya ta ƙara bankawa Inteesar harara a zuciyarta tace"me wannan ƙazamar yarinyar takeyi takeyi a office ɗin Oga da har yike dakamun tsawa".
wata zuciyarce tabata amsa da" sede in temakonta zeyi amma dai bade ya kula wannan ƙazamar yarinyar da soyayyaba".
tafita cikin sauri ta fita ganin yanda Namijin duniya yawani haɗe rai.

Tana fita yamaida sexy eyes ɗinsa kan Inteesar data duƙurshe tana zubarda hawaye yace"keeeh inkukan zakiyi ki fita waje inkingama kya shigo nayimiki abinda zan miki domin nan ba gidan mutuwa bane".
a hankali batare data haɗa ido dashi ba ta miƙe da niyyar barin office ɗin tajishi cikin muryar  isa da taƙama yace"keeh banitakardunki ingani inya dacema a ɗaukeki aikin".
a zuciyarta tace"banda kar inkoma gida Abbah ya rifeni da faɗa wallahi da bazan kula wannan tsinanneba amma yanzu yana iya tunda a office ɗinsa nike dole inkai zuciyata nesa".
sauke ajiyar zuciya tayi gefe guda kuma wata muguwar tsanar Namijin duniya taji jitake kamar ta shaƙeshi ta huta a hankali tashiga takawa harta isa gabanshi bata bari ta ɗago idanunta ba saboda gani take tunda take ba'ah taɓa muzantata irin yadda Namijin duniya ya muzantataba batare data bari sun haɗa ido ba ta kauda kanta gefe tare da miƙamasa envelop ɗin documents ɗinta a yatsune ya ansa tana kallonsa ta gefen idonta yashiga bubbuɗawa.

Seda yaɗau lokaci yana kallon result ɗinta a zuciyarsa yace"wow ammafa yarinyar nan tayi ƙoƙari pharmacy".
a fili kuma taɓe baki yayi a yatsune ya kalleta tare da cewa"anyako wannan nakine ba takardun ƙawarki kika aro ba dannasan kede yarda baki da tarbiyya bazeyiwu ki wani karanci pharmacy ba koba komai na masu kwakwalwa ne bana irinki bane masu kwakwalwar kifiba".
banza tayi dashi harya gama zancensa sannan ya miƙamata tare da cewa"kije waje seki duba inda sunanki yafito".
a fusace ta ɗauki takardunta tare yun fari da  fararen oily  eye ɗinta ta murguɗamasa small

pinky lips ɗinta tare da cewa"Allah ya isana mugu azzalumi kasamun wani ƙazamun bakinka dayasha yawon bariki a tsarkakken bakine aiba ƙarya nayimaka ba ko yanzu ka gwadamun rashin tarbiyyartaka".
taƙarasa zancenta tare da kwasa da gudu ta fice wata uwar tsuka Namijin duniya yasaki tare da cewa"zakisan nine banda tarbiyya stupid kawai aidai zaki dawo ba tafiyarki kenanba".
ya miƙe tare da kallon agogon hannunsa yaɗauki phone ɗinsa ya nufi gurin pridge ɗinsa yaɗauki ruwa yadawo yazauna ya ɓalli drugs ɗinsa yasha sannan ya miƙe ya nufi waje.

*INTEESAR POV*
Tana fita da gudu taga sakatariya ta tsareta da ƙananun idanunta tana kallonta tsaki tayi haɗe da cewa"cusu ba karjini a haka zaki ƙare a titi ke inbanda tinkiyace ma wani yaganki ai seya ɗauka dangin ogomoshoce se wani tsinanne ƙirji kike banƙaromasa  saboda rashin aji ƙirjin nakima kamar farantin fawa wama zegani harya burgeshi dan haka ina gargaɗarki niba sa'arki bace kije can ku ƙarata kedashi amma inkikace zaki sakani zan baki mamaki banza mara aji".
tana gama faɗar maganarta zata wuce kenan taji sakatariya ta tintsire da dariya tare da nunata sama da ƙasa tace"tayama za'ace classy irin Namijin duniya yasoki dubifa kayan jikinki duk a koɗe sekace mabaraciya".
"ke yadama da harkike zargin wani abu amma ni na wuce ajin wannan ɗan iskan mutumin dama sede irinku ƴan bariki karuwai da basusan mutuncin kansu ba".
tana gabama faɗamata haka ta wuce fuuu tabar sakatariya tsaye nan baki buɗe Namijin duniya dake kallon duk abunda yike faruwane yasaki wani murmushin dabe shirya yinsaba yace"gaskiya wannan yarinyar tana buƙatar general service wai ƙirji kamar farantin fawa amma bata da mutunci".
ya miƙe ya fice abunsa.

A farfajiyar Comphany ɗin taga Hauwa'uh tsaye tana jiranta ƙarasawa tayi inda take tare da dafata tace"sorry sweetheart nabarki ke kaɗai tunɗazu".
sauke wata ajiyar zuciya Hauwa'uh tayi tare da cewa"bakomai ina nan ina tinanin Allah yasa ba wani abun yayimikiba dan bakiji yadda ƙirjina yariƙa dukan tara-tara ba tunda kika shiga".
tinanowa tayi da ya haɗa bakinsa da nata saurin tofar da miyawun  bakinta tayi tare da saurin aro jarumta dankar Hauwa'uh tagane tace"kwantar da hankalinki ƙawata ba abinda yayimun kidena ɗaga hankalinki kinji".
"masha Allah se yanzu naji hankalina ya kwanta muje to gurin da ake bawa koya takardar can muji position ɗinmu dakanan semu biya gidan ɗinkinmu dan karmu rasa ɗinki next week ne bikin Muneera Musa".
"toh  muje".
nansuka nufi gurin da ake rabawa suna zuwa ana kiran sunan Hauwa'uh ansa tayi  b tare data buɗaba  tana jiran akira Inteesar a ƙarshe aka kira Inteesar suna ganin mutane nata farinciki zasu   bar gurin sukaji wata mata tana cewa ƴar uwarta"daɗina da Comphany ɗinnan indai mutum yayi karatu to zesamu muƙami babba idan kuma iya matakin secondry gareka shine za'ah ɗauke a irinsu cleaners haka da massengers Comphany ɗinnan akwai adalci".
matsawa can gefe da mutane sukayi kowanne cikinsu yashiga buɗe takardarshi gabanta ya buga damm sakamakon cin karo da sunanta a matsayin cleaner ɗin office ɗin Namijin duniya

wasu zafafan hawayene suka shiga sinitiri a idanunta cikin murna Hauwa'uh ta ɗago da niyyar magana taga halin da ƙawarta take ciki tayi saurin fisge takardar hannun Inteesar ta duba sosai taji bataji daɗiba cikin tausayin ƙawartata tace"kinga irin abinda nike faɗamiki ko a lokacinnan kika zage kikayimasa rashin kunya san ranki dama na faɗamiki baze barkiba wallahi duk gurinnan ba wanda yazo da karatun dayakai naki amma seyasa aka sakaki a matsayin cleaner a office ɗinsa".
"Sweetheart bana taɓajin ina danasani a abunda nayiwa wannan sakaran sema ƙaramun karsashi da yikeyi muje kinji".
tafaɗa tare da share hawayen dake zubomata "toh muje".
"congratulation Sweetheart kice kinzama sakatariyar Adam".
"nagode".
hararta Inteesar tayi nansuka jera suka tafi a bakin Comphany ɗin suka tsaya samun napep basu wani jima da tsayuwaba wata jibgegiyar mota tayi parking a gabansu wani matashin gentle guy ne yafito daga motar tare da zagayawa indasu Inteesar suke fuskarsa ɗauke da murmushi ba ƙaramun kyakyawa bane bakinsa ɗauke da sallama ya isa garesu haɗa baki sukayi gurin cewa"Wa'alaika salam".
"ƴammata ina zuwa haka be kamata haɗaɗɗun ƴammata kamarku suna tsaye rana na dukansuba bayan daka ganinku ba kalar shiga ranar bane".
murmushi sukayi gabaki ɗayansu Hauwa'uh tace"waya faɗamaka haka Malam".
"hmmm aiba se wani ya faɗamunba bayan ga zuciyata a kusa dake dole insani".
yaƙarasa zancensa yana kallon Inteesar dariya Hauwa'uh tayi tace"inko hakane kayi dace da zuciya mr kyau".
"aidama nasan zuciyata me kyauce kuzo muje inkaiku namanta ban faɗama zuciyata sunanaba sunana Zaid".
"a'ah mungode me napep muke jira".
Inteesar da ke tinanin muzantata da Namijin duniya yike ce ta sauke wata ajiyar zuciya wadda tasa su Zaid saurin kallonta yace"dan Allah ku shiga nakaiku kinga dakanan nasan gidansu zuciyata".
Inteesar na shirin cewa a'ah taga Namijin duniya da anbuɗemasa mota ze shiga yana kallonsu tace"toh mushiga Hauwa'uh".
nanya buɗewa Hauwa'uh baya ita kuma ya buɗemata front seat tana ɗaga ido caraf idonsu ya sarƙe dana Namijin duniya ta taɓe baki tashige ya rife ya zaga ya shiga yajasu sauke ajiyar zuciya Namijin duniya yayi a zuciyarsa yace" to wannan kuma meye haɗinta dashi da har suka shiga motarsa kenan duk abinda nayimata bataji haushi ba kenan aiko dole da sake dukda bankai ƙarshen plan ɗinba".
ɗaukar wayarsa yayi ya tura text bayan 30mins wayarsa tayi ringing ɗagawa yayi tare da yin shiru daga ɗaya ɓangaren Ahmad yace"nagani amma kasan wani abu yarinyar nan taji haushi sosai ganinka ne yasa ta nunamaka bataji haushiba plan ɗinmu yafara tafiya sucessful wallahi".
"ok to semu cigaba".
nansukayi sallama ya kashe tare da cewa driver"mu tafi".
nansuka ɗauki hanya.

Ɓangarensu Inteesar ko sun ɗanyi tafiya sannan Zaid yace"wacce unguwar zankaiku

gimbiyata".
"Suleja".
"ok amma baki faɗamun sunanki ba".
"sunana Inteesar".
"nice name ".
shiru tayi sukaita hirarsu shida Hauwa'uh tayimasa kwatancen gurin me ɗinki seda suka biya yabiya musu kuɗin ɗinkinsu dukda basusoba suka yimasa godiya sannan suka ɗauki hanyar gidansu daidai kwar gidansu ya tsaya yana gama parking suka buɗe suka fito hakan yasashi shima fitowa yana wasa da ɗan key ɗin dake hannunsa yace"Hauwa'uh se gobe kuma".
"eh Uncle Zaid".
"a'aaah godiya nike ƙawarmu ".
nantayimusu sallama ta wucetashiga gida kallon Inteesar yayi dake niyyar tafiya yace"ranki shidaɗe kitsaya inada magana".
"toh inajinka".
"da farko sunana Zaid a unguwar Garki nike sunan mahaifina Cheif Judge Muhammad Abdurrahman nagankine na yaba da nutsuwarki tunda naganki nafara murna nasamu muradin zuciyata ina fatan zaki karɓi soyayyata".
Haka nan yaji wani mugun ɓacin rai ya baibaye shi ɓangarensu Inteesar ko tana katse waya suka cigaba da tafiya bazato suka ji lion voice ɗinsa ta daki kunenta ya ce"kee! wa kika tambaya da zaki bita ko  ce miki aka yi kin gama aikinki na yau ne?".
Tsayawa suka yi cak jin abin da ya ce" ɗago oily eyes ɗinta tayi da suka fara tara ruwa ta kalli Hauwa'uh murya na rawa sabo da kukan dake tahomata ta ce" sorry sir kije Zaid na waje a fara yi miki in yaso in na tashi daga aiki sena biyoku".
"a'ah kibari na jiraki mutafi tare".
A'ah kitafi a fara yi miki a rage idan nazo ni kawai za'ah yiwa".
"toh  muje na rakaki".
Toh.
Har sun fara tafiya cikin ɓacin rai ya ce"wa kika tambaya  permission ɗin fita?".
Tsayawa tayi  cikin sanyin da jikinta yayi lokaci ɗaya ta ce "sorry sir kije besty sena taho idan kuma yamma ta cika yi ba lallai nazoba semu nazo ba sena kira ki sanar dani gidan kwalliya nazo na sameku".
sosai  taji tausayin ƙawarta na ratsa zuciyarta ta ce"toh".
Ta tafi tabar Inteesar komawa tayi ta tsaya ɗan nesa da in da suke zau ne tana share hawayen dake ƙoƙarin zubo mata a zuciyarta tana dana sanin biye masa da tayi a rayuwarta har suka gama hirarsu tsawon lokaci tana tsaye suka miƙe zasu tafi Adam ya ce"se mun haɗu anjima mu yan zu zamu wuce".
Basu hannu Namijin duniya ya yi tare da ce wa"toh sai mun haɗu a gurin dinner dan akwai wani abu da zan ƙarasa idan kun shirya mayi waya".
Toh shi kenan".
Nan suka tafi suka barshi daga shi se Inteesar shiru office ɗin ya ɗauka na tsawon wani lokaci ba abin da kake ji se ƙarar a.c da keta faman aiki kallon yadda ta takure alamun a.c tayi mata yawa yayi tare da taɓe baki ya miƙe ya koma kan kujerarsa ya kunna system ɗinsa ya shiga kallon wani series na ƴan korea me suna Play full kiss yama manta da wata Inteesar daketa faman tsaiwa kamar wadda ta haɗiyi taɓarya yanata faman doka smile da alama film ɗin yana kai masa a hankali ta ɗago lulu eyes ɗinta daketa zubar da ruwa ta kallesa gani tayi kallonsa ma yike yi hankalinsa kwance yama manta da ita ga ƙafafunta daketa faman zafi sabo da tsayuwa da taketa yi wani mugun tausayin kanta ne ya kamata a haka ta cigaba da tsayuwa ba tare data nuna tagajiba ko wani sauyi a fuskarta lokaci zuwa lokaci tana share ƴan kwallolinta .

Wuraren ƙarfe biyar ya shigo office ɗin fuskar nan ba annuri  a ciki-ciki ya ce"salamu Alaikum".
"Wa'alaika salam sannu da dawowa".
Taɓe baki ya yi ba tare daya amsa mata ba ya wuce ya zau na akan kujera ya ce"kya iya tafiya".
Cikin sanyin murya ba tare data nuna ta damuba ta ce"thank you sir".
Tafaɗa muryarta na rawa da kyar take iya ɗaga ƙafarta sabo da tsamin da tayi mata ga wani jiri da yike ɗibarta luuu ta tafi zata faɗi tayi saurin dafa bango Namijin duniya dayasa hannu ze da

niyyar tareta saurin matsawa gefe tayi tare da cije ɗan pinky lips ɗinta murya na rawa sabo da kukan daya fara taho mata ta ce"nagode sir".
 Tana gama faɗan haka tashiga tafiya cike da jarumta duk da irin yadda take jin ƙafafun na mata azaba haka ta daure ta tafi abunta tana kuka.

Ji ya yi duk beji daɗin yadda ta fita ba tana kuka domin jin kukanta yike har cikin zuciyarsa be san meya saba ji ya yi beyi mata adalci ba kome ya tino kuma ya ɗaga kafaɗa alamar matsalarta ce ya cigaba da aiki a system ɗinsa  ɓangaren Inteesar ko tana fita taga wani gangarumin hadarine a garin ga wata irin iska da akeyi ba alamun abun hawa ko kaɗan ta daɗe tana jiran abun hawa kafin dabarar kiran Zaid ta faɗo mata saurin zaro wayar da Zaid ya bata tayi daga cikin jakarta tashiga dialing no  Zaid a kashe taji wayar a kashe hakan yasa hankalinta mugun tashi tashiga  rage tafiya ko Allah ze sa tasamu abun hawa har tayi tafiya me nisa amma bataga masu napep ba samun guri tayi ta raɓe ta tsugunna kamar wata marainiya ta fashe da wani marayan kuka.

Bazato taji  ana mata horn ɗago sexy eyes ɗinta tayi da suka rine sabo da kukan da take yi ta saukesu akan wata haɗaɗɗiyar  farar G-box tasha tintac se ɗaukar ido motar take yi mai da kanta tayi ta cigaba da kukanta dan tasan da Zaid ne ze kirata ta cigaba tana cikin kuka taji muryar wani mutum akanta ya ce"ki taso mutafi inji sir".
 Ɗago jajayen idanunta tayi ta saukesu akan mutumin wan da daka ganin shi kaga security ta ce"waye ogan naka?".
Zai yi magana  kenan ya ji wayarsa na ƙara ɗagawa ya yi tare da ce wa"okay sir".
Ya kashe wayar tare da kallonta ya ce"ya ce in ba zaki taho mutafiba inkyaleki".
Waigawa tayi taga unguwar kwal ga duhu ya ɗan fara yi bako mutum ɗaya hakan ya sata miƙewa jiki ba kwari tabi bayan mutumin ƙofar baya ya buɗe mata tashiga ya mai da murfin ya rufe sannan ya zaga ya shiga mazaunin driver ya jasu.

Tana shiga daddaɗan ƙamshin turarensa ya daki hancinta satar kallonsa tayi ta wutsiyar idonta gani tayi yana karatun daily trust ya ɗora ƙafa ɗaya kan ɗaya saurin juyar da kanta wajan window tayi tare da ɗan tsuke ƙaramin bakinta a zuciyarta ta ce"shi dai ko a ina zamansa kenan sabo da isa".
Tana cikin wannan zancen a zuciyarta taji lion voice ɗinsa ta daki dodon kunnenta ya ce"me yasa baki kira wannan faƙirin saurayin naki  ya ɗauke ki ba? Ko yau be aro motar bane?".
Sosai maganganunsa suka ɓata mata rai amma seta make tayi kamar ma bata san da ita yi keba jin tayi banza da shi yasa ran shi ɓaci ya yi kwafa ringing wayarta tashiga yi ɗauka tayi tare da ce wa"tun ɗazu nayi ta kiranki baki ɗauka ba".
Sorry besty ina wanka ne kin taho muna gurin me make-up ki wuto kawai na faɗawa Umma na

tafi miki da kayan da zamusa".
Anya zanyi make-up ɗin nan ma ni kuwa kin san bana son a cika mun fuska kin tafi da Khadijah ko".
Ai ko dole kiyi kin san Asma'uh bazata ji daɗi ba ki daure kawai kiyi eh na taho da ita amma fara yi mata make-up ɗin Uncle Zaid ya yi mana siyayya sosai ki kira shi kiyi mishi godiya kowacce cikinmu yasiya mata gown da takalmi da pos se kuma dalleliyar waya ƙirar iphone 13pro daya bani in ajiye miki".
Cikin farin ciki ta ce"dan Allah".
Wallahi kinga ko dole kiyi kwalliyar nan ko dan kiyi masa hotuna".
Sosai ma kuwa  aiko bara in kira shi in yi masa godiya kuwa".
Ya dai kamata sekin ƙaraso muna gurin Reality ".
"toh sena ƙaraso".
"yauwa".
Nanta kashe cike da zumuɗi tafara lalubar no Zaid taji muryarsa ya ce"ki faɗa masa unguwar da za'ah kaiki".
Se lokacin ta tina a in da take hakan yasa fara'ar dake kan fuskarta saurin gushewa ta katse kiran da take yiwa Zaid ta ce"kusa da Garki akwai wata me make-up a tsallaken titi nan zan sauka".
Toh ranki shidaɗe".
ce war security nan ya juya akalar mota suka nufi Garki shiru ne ya biyo baya har suka isa suka yi parking a ƙawataccen gurin tanƙamemen shagon make-up ɗin Real Eeshow juyawa tayi ta kalli Namijin duniya cikin girmamawa ta ce"thank you sir".
Ba tare daya ɗago daga karatun daily trust ɗinsa ba ya yi banza da ita buɗe mata mota security ɗin ya yi ta fita tare da shigewa gurin driver yaja motar suka bar gurin.

8:30Pm
Suka iso gurin dinner kallon Inteesar Hauwa'uh tayi ta ce"amma gaskiya besty kinga yadda kika yi kyau kuwa kamar bake ba kodon bakya make-up shiyasa yau da kika yi ya yi mugun yi miki kyau".
Hmm besty kenan niko kunyar fita nike yi cikin mutane da wannan kwalliyar sabo da idan naga ana kallona duk se in tsargu bakiga yadda kika yi kyau ba Wallahi besty".
"au nice banyi kyau ba kenan ko Aunty?".
Sorry my Khady nina isa in ce  da wannan shagaɓaɓɓiyar ƙanwar tawa bata yi kyauba? Kinfi kowa yin kyau".
Yauwa Auntyna muje".
nan suka fita Inteesar ji take kamar tsirara take sakamakon rashin saka gyale da batayi ba kanta a ƙasa sabo da wata irin kunya da take ji haka sukabi layin da akai na shigar da amarya suka shiga tanƙanemen hall ɗin da ya gaji da haɗuwa suka fara tafiya kiɗa na tashi har suka raka amarya da ango mazauninta dafa Inteesar Hauwa'uh tayi cikin ƙasa da murya ta ce"kinsanko waye angon Asma'uh".
"a'ah waye".
"Sir Adam ne".

dammm ƙirjinta ya bayar lokaci ɗaya zuciyarta tashiga bugawa da sauri-sauri ga yawun bakinta daya ƙafe ƙaf murya na rawa ta ce"what?".
"Eyi".
Wani gumi ya shiga ketomata suka samu seat suka zau na ta ce"amma baku kyauta mun ba da kuka hanani saka gyale ko wanne tom and jerry ya gama kallemun jiki a banza".
Nan Hauwa'uh taita kwantarmata da hankali aka shiga gabatar da program.

Suna cikin hirarsu da Khadija taji muryar m.c na ce wa"muna buƙatar aminiyar amarya me suna Aishatu domin tazo ta gabatar mana da tarihin amaryar".
a gigice ta ɗago ta ce"Hauwa'uh kinga irin abin da nike gudu ko da kun barni nasa gyalena ai da duk haka bata faru ba".
"Sorry besty gani muka yi idan kika sa zaki lalata kwalliyarki kiyi haƙuri kije kiyi kin san Asma'uh bazata ji daɗi ba".
"Ba bu 'in da zani ".
Ji suka yi m.c ya ƙara kiran sunan Inteesar hakan yasa Khadija ce wa"Aunty dan Allah kiyi in baki yi ba kamar kin watsawa Aunty Asma'uh ƙasane a ido ta  wuce kowa ta zaɓeki  plz Aunty".
taƙarasa zancenta tare da saka hannunta alamar roƙo kamar zata yi kuka hakan yasa Inteesar ce wa"sorry my Khady karkiyi kuka bara naje".
"yauwa Auntyna maganin kukana".
nan Inteesar tafara tafiya cikin nutsuwa take tafiya kanta a ƙasa hankalin kowa kanta ya koma sakamakon m.c daketa koɗata tun daga nesa ya kafeta da shanyayyun idanunsa da sukayi kama dana me bacci gani yike kamar ita kamar ba itaba hakan yasashi  tanfatsar da glass cup ɗin dake hannunsa hakan yaja hankalin mutanen dake kusa da gurin  yi ke suka kalle shi ba tare daya sani ba a zuciyarsa ya ce"why zuciyata da zaki dameni da tunanin wannan kucakar yarinyar ne da kowacce nagani ganinta nike kamar ita why anyako wannan yarinyar ba mayya bace takamani".
yana wannan tunanin harta ƙarasa gurin m.c ta tsaya saurin dawowa ya yi daga tunanin daya tafi gani ya yi ba Imergination ɗinta daya saba yi bane ita ce tasha gayu tagaji da haɗuwa se ƙamshi take bazawa!!!!!!!!!

meson shiga group ɗin wannan novel ɗin tayimun magana ta wannan number 08108362334

Votes and Comments
Plz share

_*Daga Alƙalamun Ƴar Mutanen Gwarzo.*_r Mutanen Gwarzo.*_🌻 *MAN OF THE WORLD* (NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK 1*

*PAGES*1️⃣9️⃣➡️2️⃣0️⃣

Cikin amsa kuwwa m.c yace "masha Allah ga babbar aminiyar amarya amma gaskiya tahaɗu kwarai dagaske bara muji taƙaitaccen tarihin babbar aminiyartata".
yaƙarasa zancensa tare da miƙawa Inteesar laudspeaker amsa tayi tare da ɗago da kyakyawar fuskarta wadda tayi mugun kyau domin inba farin sani kayimataba ba lallai bane ka ganetaba saboda kwalliyar tayi mugun amsar jikinta kamar ka saceta ka gudu jin abinda m.c yafaɗane yasashi ƙara tabbatarwa da kansa tabbas ba gizo tayimasa ba itance dai zuciyarsa ce tacemasa"to a ina tasamu kuɗinda harta iya saka wannan tsadadden material ɗin domin nidai a iya sanina bamasu hali bane".
wata zuciyarce tace"wataƙila saurayinnan natane ya siyamata".
tsaki yayi saboda lokaci ɗaya yaji wani mugun ɓacin rai yadirarmasa lokaci ɗaya yaji duniyar tayimasa zafi Mimah dake zaune kusa dashi ce tace"wow Hubbi ammafa ƙawar amaryarnan kyakyawace ajin farko".
taɓe baki Namijin duniya yayi kamar wanda yaga kashi ya waigar da kansa gefe yadda bama zaka ɗauka yaga Inteesar ba.

Cikin zazzaƙar muryarta me tafiya da zuciyar duk wani ɗa namiji me lafiya tashiga zazzaga speach kamar wata baturiya yadda take ba kowacce kalma haƙƙintane yasa taƙara burge mutanen gurin uwa uba kuma a natse take komai nata bayan ta gama da yaren turanci ta juya larabci yadda take fitar da harufa bazaka taɓa ɗauka ba balarabiya bace tana gamawa gabaki ɗaya gurin ya kaure da tafi saboda baƙaramun tafiya da hankalin mutane tayiba ta juya zata tafi m.c yace"ranki shidaɗe kitsaya babban abokin ango yazo yabada biography ɗin ango sannan ku zauna a seat ɗin da aka tanaza dominku munason ganin babban abokin ango ɗaya tamkar da dubu uban gayya Sir Abdallah Namijin duniya ".
damm ƙirjin Inteesar yabayar jin sunan wanda aka kira lokaci ɗaya hankalinta yayi mugun tashi amma dayike miskilace bazaka taɓa fuskanta ba tafi gurin ya ɗauka alamun Namijin duniya ya miƙe a hankali ta ɗago lulu eyes ɗinta da suka cika da tsoronsa ta saukesu akansa ɓangaren Namijin duniya ko yanajin abinda m.c yafaɗa yaƙara shan kunu ya ɗauki glass cup ɗin dake

kusa dashi kenan yaji wasu abokan kasuwancinsu ɗaya na cewa ɗaya"wow amma gaskiya wannan babe ɗin ƙarshe ce anyako bazan raɓa ba kuwa".
"gaskiya dai Muhseen kayi maza ka raɓa domin tahaɗu yarinyar tunkafin wani ya rigaka domin irin wa'innan sune irin matan da ake layi gurin neman aurensu se me tsananin rabo kesamun aurensu kagafa ga kyau ilimin addini da boko ga nutsuwa uwa uba hankali kai Muhseen inka sameta kagama morewa wlh ga dirin jiki".
"ai da wuri zanyi sauri inje ana tashi zanje insanarmata da kudirin zuciyata ko Allah zesa insamu shiga da aduniya zanga nafi kowa sa'ah".
lokaci ɗaya yaji wani ɓacin rai ya lulluɓesa idanunsa sun canza kala saboda tsananin ɓacin ransu yayi saurin ɗaukar glass cup ɗin ya shanye ruwan tas kozeji sauƙin zugin da zuciyarsa kemasa amma wani canji ga wani abu daya tsayamasa a zuciya na ganin irin shigar dake jikinta .

Sanye yake da white arman suite wanda sukayi matuƙar amsar jikinsa se necktiet ɗinsa data kasance baƙa sumar kansa kamar kullum se sheki takeyi anyimata irin askinnan na zamani wanda an aske gefe da gefe anbar tulun suma a tskiya wadda taketa ɗaukar ido da sajensa tamkar wani balarabe kunnensa sanye yike da ɗan kunne me matuƙar ɗaukar hankali ga wasu shegun sarƙoƙi daya saka suka zubomasa har ciki cike da isa da izza yike tafiya yayinda hankalin ƴammatan gurin gabaki ɗaya yayi kansa saboda a ƙasarma gurin ƴammata haka suke cemasa burin kowacce ɗiya mace ƙarasawa yayi inda Inteesar ke tsaye a hankali ta ɗago fararen sexy eyes ɗinta da niyyar satar kallonsa caraf idanunsu ya sargafe cikin na juna saurin janye idanunta tayi a nasa tare da yin ƙasa da kanta ta ƙarasa inda yike cikin ladabi ta miƙamasa laudspeaker ɗin hannunta bazato taji lallausan hannunsa ya haɗa da hannunta wani irin shock ne ya ziyarci gabaki ɗayansu hakan yasa tayi saurin janye lallausan hannunta a nasa cike da izza gami da taƙama yashiga bada biography ɗin ango yana gamawa gurin ya ɗauki tafi jin yagama sanya Inteesar fara tafiya ba zato taji hil ɗin takalminta ya tafi luuu zata faɗi saurin rife zara-zaran eye lashes ɗinta tayi saboda tarigada tagama sadaƙar da zatajita a ƙasa bazato tajita a jikin mutum wata wawuyar ajiyar zuciya suka sauke a tare sexy eyes ɗinsa da suke kamar na me bacci ya sauke akan zara-zaran eye lashes ɗinta da suka kwanta kamar na kanti sunsha lining da baƙin kwalli ga eye shadow da suka sha lokaci ɗaya yaji tsigar jikinsa ta tashi yarrrr idanunsa sun wani ƙanƙance irin na wa'inda suka kai ƙololuwar buƙatuwa a hankali yashiga yawo da sexy eyes ɗinsa kan kyakyawar fuskarta ya shagaltu da kallonta ɓangaren Inteesar ko jin bata faɗi a ƙasa bane yasa tashiga buɗe oily eyes ɗinta ta saukesu kan kyakyawar fuskar Namijin duniya lokaci ɗaya gurin yaɗauki tafi domin baƙaramun bada style sukayi ba idan kagansu seka ɗauka couples ne saboda matching ɗin da sukayi kallon-kallo suka shigayi hakan yayi daidai da ɗauke wutar gurin bazato taji ya manneta da faffaɗan ƙirjinsa da kowacce ɗiya mace ke burin jinta a gurin saurin haɗe fuskarsu yayi gurin ɗaya yayinda dogayen hancinansu suka haɗe guri ɗaya a tare suka saki wata nannauyar ajiyar zuciya jikinta ne yashiga rawa saƙala kansa yayi ta jikin wuyanta yashiga shinshina wuyanta da kamar anyimasa ɓarin turare akaikai yashiga sauke ajiyar zuciya wadda daga ita seshine kawai sukeji bazato taji saukar numfashinsa daidai kunnenta cikin narkakkiyar muryar dabata taɓajin yayi

magana da irinta ba kamar yana yimata raɗa yace"waya baki izinin saka irin wa'innan banzayen kayan keko kunyar fitowa  a haka bakijiba jibi wata kwalliya kamar wata aljana kewai a tinaninki kinyi kyau  dama zuwa kikayi kika wanke dayafimiki alheri domin mutane dariya suke tayimiki a hakan kike cewa wani bashi da tarbiyya ke ai itan gareki domin dai duk mace me aji datasan darajar kanta bazata saka irin wannan kayan ta fito cikin taron jama'ah ba jibeki kamar wata one ko lankwasa babu".
sosai ranta yakai ƙololuwar ɓaci dashi ta matsar da bakinta daidai kunnensa zatayi magana  taji yayi saurin haɗe bakinsa da nata seda ya shanye jambakin bakinta tas sannan ya zame bakinsa a nata cikin muryar raɗa yace"da kinwani saka jambaki kamar wata buranya ke dan bakiga irin munin da kikayi bane temakonkifa nayi domin banaso ina ganin mutane suna miki dariya keko bikiyardaba se wani yanga kikeyi ala dole gani kike kinyi kyau".
a zuciyarta tace"kodai banyi kyau bane dagaske shiyasa naga mutane nata kallona ne bara zan tambayi Khady naji".
a filiko sosai ranta yakai ƙololuwar ɓaci dashi ganin yadda yaketa tattaɓamata jiki bako sisi a sanga hakan yasa tasa hannuwanta da iya ƙarfinta ta tureshi ta sassauta murya yadda iya shikaɗaine zejita tace"to ina ruwanka idanma banyi kyanba kokai ka  biyamun" .
"wayema zeyi ɓarnar kuɗinsa kan wannan mummunar fuskar taki dako taushi bata dashi ƙabe-ƙabe take kamar bayan kada ayimiki kwalliya sede wannan ɗan asaran saurayin naki dayaga ze iya".
sosai ran Inteesar yakai ƙololuwar ɓaci idanunta suka fara kyallin fito da ruwa zatayimasa magana kenan wani diff haske me circle yafito a inda suke yayinda wani cool music yashiga tashi bazato taji hannunsa a waist ɗinta yashiga yin rawar nan ta turawa ya wurnata can yayi can da ita kamar wata ƴar baby ganin mutane na kallonsu ne yasa ba yanda ta iya tabishi sukayi rawar bayan sun gama  aka dawo da haske ɗaukar tafi gurin yayi lokaci ɗaya suka nufi high table suka zauna yayinda Inteesar tazauna nesa da Namijin duniya.

"Feenerh wai wannan wacce tsinanniyar yarinyarce dahar ta haɗa jiki da Namijin duniya kina zaune Feenerh".
" hmm Zuby kenan to itace sabuwar cleaner ɗinnan danake baki labari kike ganin kamar bata da abinda zata siyi zuciyar Namijin duniya to gadaishi kingani da idanunki har rawa yayi abinda nike burin inyi da Namijin duniya shi wannan kwailar tayi to kindai gani da idanunki keda dabiki ɗauki zancennan serious ba ni dama tunda tazo gurinnan naji na tsaneta wallahi".
sosai ran Zuby yaɓaci a zuciyarta tace"dole inyi maganin duk wanda ze kawomun cikas a rayuwata dakai Abdallah domin kai nawane ni kaɗai ba wata ɗiya mace data isa inyi sharing ɗinka da ita ban kauda itaba".
a filiko sosai ta nuna ɓacin ranta ta dafa kafaɗar Feenerh cikin nuna alhini tace"aiko ƙawata dole muɗauki babban mataki akanta bata isa tazo da rana tsaka ta rabaki da abu mafi soyuwa a garekiba ko itaɗin banza kinkoyi amfani da maganin dana kawomiki kuwa".
"sosaima kuwa amma kinga shiru anyako maganin bokannan kuwa yanayi Zuby domin ni banganin wani canji ko ɗaya".

damm ƙirjin Zuby yabayar amma dake ƴar duniya ce seta make tace"yikai domin bokannan kaf inda su Ummanmu suke zuwa ba wanda yakaishi aikinsan irin wannan aikin ba'ah yimasa garaje kibari mugani nanda sati uku".
"toh mujira amma yanzuma semunje munyiwa wannan kwailar kashedi".
"toh  kibari a tashi".
nan sukaita tsinewa Inteesar.

Ɓangaren Mimah ko sosai rawar dayayi da Inteesar ta ƙonamata rai hakan yasa takira Mum  a waya kamar zatayi kuka ta zayyanemata abinda yike faruwa daga ɗaya ɓangaren Mum tace"ki kwantar da hankalinki duk duniya Abdallah bashi da wata mata data wuceki ko ubansa be isaba bareshi me akai akayisa dazaki tsaya kina zubarmun da tsadaddun hawayenki  ki kwantar da hankalinki karki nunamasa kinji haushin abinda yafaru kinjini ninasan yadda zanyi dashi".
"to Mum".
nanta kashe ta goge hawayenta tayi kamar ba abinda ke damunta.

Sosai aka shiga gabatar da program yayinda gawurtattun masu kuɗi sukaita ɓarin naira kamar basaso har akazo yanka cake ango ya gutsura yabawa amaryarsa a baki itama amarya ta gutsura tabawa ango matsawa Inteesar tayi ta yanko cake ɗin da niyyar bawa Asma'uh yazuba akan tsadadden takalmin Namijin duniya jikinta ne yashiga rawa sakamakon ganin kan takalmin wanda cake ɗin ya zuba lokaci ɗaya oily eyes ɗinta suka tara ruwa murya na rawa tace"sorry Sir".
ɓangaren Namijin duniya ko sosai ranshi yakai ƙololuwar ɓaci a tinaninsa dagangan tayimasa haka saboda ta tozartashi ne gaban abokansa hakan yasa zuciyarsa ta hassala ba abinda yike se huci  hakan yasashi zama kan wata resting chair ya ɗaga idanunsa da suka rine saboda tsananin ɓacin rai yazubawa Inteesar da zuwa wannan lokacin hawaye yagama wankemata fuska saboda tsabar tsoron hukuncin dazemata murya na rawa taƙara cewa"sorry sir wallahi bansan yazubarmaka akan takalmiba".

Saurin ɗagamata hannu yayi cikin ɓacin rai gamida isa da izza a gadarance yace"kima bar ɓata bakinki gurin bani haƙuri domin bazan taɓa haƙuri ba sena hukuntaki daidai da abinda kikayimun saboda bakisan darajar kuɗiba shiyasa kika samun wannan ƙazamun hannun naki mara tsarki  kika lalatamun takalmi kee wacece".
wasu zafafan hawayene suka shiga sinturi akan kumatunta jin irin rashin mutuncin da yikemata dakyar ta yaƙi zuciyarta dan batason ta biyemasa su raba hali cikin muryar kuka tace"kayi haƙuri sir wallahi bansaniba".
taɓe baki Namijin duniya yayi a gadarance yace"kisa harshenki ki lasheshi  na jikin takalmina inkinaso in haƙuri kafin na irga uku ki lashe".

yaƙarasa zancensa tare da ƙara haɗe fuska jin abinda yace baƙaramun girgiza mutanen hall ɗin yayiba  a hankali ta duƙa da niyyar lashe cake ɗin kowa yabada attention ɗin lashewa zatayi wasu daka cikin mutanen hall ɗin sun rirrife idanunsu saboda tausayin data basu  se buɗe ido sukayi sukaga bata tabar hall ɗin gabaki ɗaya sosai ran Namijin duniya yakai ƙololuwar ɓaci ɗaga idannan dazeyi yaga wata me kama da Inteesar tasa hanky tana sharemasa cake  ɗin cikin sanyin murya tace"kayi haƙuri sir".
tana gama faɗin haka tabi bayan ƴar uwarta hakan yasa Namijin duniya ya fice a hall ɗin rai ɓace.

Zaune suke a gaban boka Tsula Uwar gwarama na zayyanemasa labarin Zaid wata uwar dariya Boka Tsula yayi tare da gintseta lokaci ɗaya yace"base kin ƙarasa ba ki kwantar da hankalinki indai kan wannan ƙaramun alhakine  indai zaku cika sharaɗan dazan gindaya muku auren Jamilah da Zaidu kamar an ɗaura ne ammafa sede muci galaba akan Zaidu  amma wannan sheɗaniyar yarinyar kullum setayi addu'ah shiko yanada sake da ita".
tsaki Uwar Gwarama tayi haɗe da cewa"ai wannan munafukar uwartata kullum seta sasu a ɗaki inajinsu sunyi ai  so nike boka duk yadda za'ayi ayi banaso yaronnan  ya auri yarinyar nan saboda naci alwashin indai ina numfashi kozan rasa zanin ɗaurawa bazan taɓa barin jinin Aminah yaji daɗin duniya ba seda su gani a wajen wani badai su ba boka kayi koma menene zan aikata nidai buƙata tabiya".
wata uwar dariya boka Tsula yaƙara fashewa da ita lokaci ɗaya ya ɗaure fuska cikin muryasa mara daɗin sauraro yace"sharaɗi na farko shine yau dole in sadu da Jamilah domin akwai wani magani dazan zubamata a jikinta se abu na biyu kuma zan baku wani turare da zatayi hayaƙi dashi zakusha mamaki domin Zaidu zezama tamkar raƙumi da akala tsakaninsa da Jamila  se yanda ta juyashi abinda nikeso daku dole inkunyi turaren ya shaƙa inba hakaba akwai gagarumar matsala matsawar be shaƙaba".
 wani daɗine ya mamaye zuciyar Uwar gwarama tace"ai boka indai wa'innan ne sharuɗan ba wata matsala bara nabaku guri kaji daɗin zubamata maganin dakyau sannan zamuyi turare dolensa ma ya shaƙeshi dan ubanshi be isa ya lalstamun shiriba  Jamilah ki saki jikinki da boka Tsula sosai saboda ya zubamiki maganin sosai yadda lokaci ɗaya mejan kunne ze manta da wannan  sakaran yarinyar".
"Toh Ummah kinsandai zan iya  bada komai nawa matsawar burina zecika na auren mejan kunne".
"yauwa tawan".
nanta miƙe ta fita baki bukkar boka Tsula ta barsu acan suna sheƙe ayarsu  bayan 1hr sega Jamilah ta fito daka bukkar tana gyara zani taƙarasa gurin Uwar gwarama tace"ga na turarenma yabani  da kuma wannan wai a barbaɗa a ƙofar ɗakinsu Inteesar ta tsallaks Ummah ".
"yauwa ƴar albarka ki kwantar da hankalinki zakisha mamaki yanda lamari ze canza lokaci ɗaya".
"yauwa Ummah na ina alfahari dake".
"nima haka muyi mutafi dare nayi ".
"toh".
nansuka tafi kowannensu zuciyarsa cike da farincikin samun nasara da suke fata.

10:30pm
Tunda yakoma guest house ɗinsa ba abinda yike ss faman safa da marwa yike yana tinanin irin mummunan matakin daya kamata ya ɗauka kan Inteesar katse shirun da sukayi Ahmad yayi ta hanyar cewa!!!!!!

Votes and Comments
Plz share to others

*Soyayya ɗaya da zaki nunamun sister idan kin gama karantawa kiyi sharing zuwa group goma da kike dashi  shine kawai zansan kinayi na over kamar yadda nike yinku over.*

_*Daga Alƙalamun🌻  *MAN OF THE WORLD*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK 1*

*PAGES*2⃣1⃣➡2⃣2⃣

"Wai yanzu meye abunyi ne yarinyar nan takai maƙura gurin rainaka fa ace tana ƙasanka saboda rainin hankali kasata tayi abu taƙiyi a gaban bainar jama'ah saboda ta nunawa duniya irin rainin data yimaka dole wannan karon mu ɗauki mumman mataki  akanta seta yi danasanin

saninka a rayuwa ko ya kace Adam".
"maganarka gaskiya ce  Ahmad  dole musan abinyi gaskiya".
" ni ina  ganin meze hana musa a yaran Namijin duniya suyi raping ɗinta  ina ganin shine best solution".
tunkafin yaƙarasa maganarsa Namijin duniya ya juya garesa a fusace cikin yanayin  da tun tasowarsu basu taɓa ganinsa a cikiba sukaji yace"what anya Ahmad ko kanada hankali kuwa raping ɗinta fa kace aiko wani naga yana niyyar lalatamata rayuwa se inda ƙarfina yaƙare  bare nida kaina insa Allah yakyauta in ƙanwarka ce zakace ayimata hakane ".
jin yadda yaketa huci ne yasasu kafesa da ido dafashi Adam yayi yace"calm down my man irin wannan harzuƙa haka sekace  wata ƙanwarka ko matarka  kabari ayimata abinda harta mutu bazata manta dashi ba a ganina bekamata ace da class ɗinmu da komai ba mu tsaya ƴar wannan ƙaramar alhakin tana rainamana hankali ba duka nawa take da har zamu dinga westing time akanta kaga malam ko kanaso ko bakaso dole haka za'ai gwara ayi a wuce gurinta ni ina tinaninma ni zansa a ɗakkowa ita na mori wannan shegen jikinnata me mugun tayarwa da mutane hankali dama na daɗe ina sha'awarta".
"haba  Adam kayi kaɗan kamar ba amarya za'ah kawomaka ba jibi kabarni inshana kawai  sede inmu duka zamu mora domin nima na daɗe ina kwaɗaituwa da wannan karuwan jikin nata baza'ah barni a bayaba bara na kira   Damisa  su ɗakkomana ita yau da ita zamuyi kodumo koya kace Adam".
" hakan yayi amma kuma wani hanzari ba guduba inyana ganin wannan shawarar bata yimasa ba meze hana yabi tawa shawarar ta baya ".

Sosai ran Namijin duniya yakai ƙololuwar ɓaci lokaci ɗaya idanunsa suka sauya kala yayinda jijiyoyin kansa suka tashi ruɗu-ruɗu saboda yasan halin abokan nasa indai sukaga yarinya ko ɗiyar uban waye sesunsa anɗakkomasu ita ɗago jajayen idanunsa yayi  ya zubawa aminan nasa cikin takaici yace"ya isheku haka banason irin wannan zancen banzan naku kuma wallahi duk wanda kukasa ya ɗakkota sede uwarsa ta haifi wani  domin indai ina numfashi bazan taɓa bari wani ya ɓatamata rayuwa ba".
mamakin yadda ya haƙiƙance yanata  zazzaga musu masifa  ne yakama su Ahmad domin tunda suke a rayuwarsu basu taɓa  ganin Namijin duniya a cikin irin wannan  halinba dafashi Adam yayi yace"anya ko abokina baka kamuba kuwa a tinanina inkaji wannan shawarar  tamu murna zakayi  amma se mukaga akasin haka saboda irin abinda yarinyar nan takemaka yayi yawa dukfa abinda kaga munayi saboda  farin cikinka mukeyi badon wani ba".
A matuƙar fusace yace"Wannan ba mafita bace  face shawarar banza data wofi   wadda zata kaini ta baroni wannan shine abu mafi muni da ƙazanta wanda zaku aikata acikin rayuwarku domin  narantse da wanda raina ke hannunsa idan ɗaya daga cikinku yayi kuskuren taɓa koda tafin hannunta ne  sena salwantar da rayuwarsa dan bazan nuna nasankuba wlh sena nunamuku true colour ɗina  dan zanbaku mamaki  a duk biye-biyen matanku bantaɓa sakamuku bakiba dan haka salin alin idanunku subar kan wannan yarinyar inba hakaba zakusan wanene Abdallah".

Da mugun mamaki suke Kallonsa jin furucinsa kasa furta komai sukayi se kallon dake nuni da tsantsar al'ajabi  da suke binsa dashi   baka jin ƙaran komai face saukar numfashinsa  da yike fitarwa kamar wani mayunwacin zaki  ganin irin kallon da suke binsa dashine yasa a zuciyarsa yace"ni Abdallah meke damuna ne mena faɗamusu naga suna bina da kallon mamaki na rasa meke damuna kan wannan kucakar yarinyar ne".
 dake miskilin ƙarshene bazaka lura da yanayin da yike cikiba sema wani ƙara shan kunu daya ƙara ajiyar zuciya Ahmad ya sauƙe kana yakafe sa da idanu na wasu mintuna  ahankali ya furta "kadde kafara sonta my man".
Wani banzan kallo ya watsa masa cikin haɗa girar sama data ƙasa yace"Banason maganan banza Meyakawo maganar so aciki wannan zancen  kuma".
Adam da mamaki ya gama cikasa ne yace"Daga cikin kalamanka za'ah fahimci akwai kishin yarinyar me ƙarfi a tare dakai domin  badan soyayyaba babu abinda zesa kafaɗa mana magana irin wannan wadda tun tasowarmu baka taɓa faɗamana ba ".
ajiyar zuciya ya sauƙe se yanzu ya tuna irin abinda yayiwa aminan nasa dafe kai yayi tare da cewa "Babu ɗigon soyayyarta acikin zuciyata hasalima tsanarta nakeji me tsanani ko wa'inda suka fita ajima ban kulasuba ma bare wata ita kona rasa matar aure bazan taɓa auren wannan kwailar yarinyar ba wadda ko  ƙirjin kirki bata dashi wa'inda suka fita komaima basa gabana bare wata bera irinta anma ku tuna lefin data aikata be kai in ɗauki irin wannan hukuncin akantaba baya ga haka bazanso ace anyiwa ƴata ƙanwata ko matata irin wannan ba shin Mezesa Ni na ruguzawa wata rayuwarta  duk abinda nayi nayisa ne domin tana ƙarƙashina banaso ta ɓatamun suna a idon duniya ".
Kai suka jinjina cike da gamsuwa da kalamansa Murmushi Ahmad yayi yace"Wallahi har nayi zaton ka faɗa tarkon ƙaunarta ".

Taɓe baki Namijin duniya yayi tare da shafa lallausar suman kansa data sha gyara yace"Allah ya kyauta wa'inda suka fita komaima basu isheni kallo ba bare ita banason haka mubar wannan zancen".
"sorry my man kawo kunnenka kaji wata hanya mafi sauƙi data kamata muyi maganinta cikin sauƙi ba tare da tashin hankali ba".
"ok".
nanya  matsa Ahmad ya raɗamasa magana a kunne wadda nikaina real eeshow banji me yike cemasa ba se gani nayi Namijin duniya ya saki wani killer smile wanda shikaɗai yasan ma'anarsa  bayan wani lokaci suka miƙe suka nufi gida zuciyar kowannensu cike da farin cikin samun mafita akan Inteesar.

Ɓangaren Inteesar ko tunda ta dawo gida take kuka hankalin Khadijat yayi mugun tashi ganin

yadda ƴar uwarta keta kuka taƙi magana  murya a raunane Khadijat tace"Auntyna wai yaushene zaki dena zubar da tsadaddun hawayenki akan abubuwan da basu taka kara sun karya bane sanadin kukannan naki yasa ƙannenki  a gida sun rainaki a wajema kina niyyar kijawa kanki wani rainin ganin kinamasa kuka shiyasa yike ƙara rainaki dan Allah abinda nike so dake ko yayimiki abu dukmun ɓatamiki ran daya yi karki ƙara nunamasa ko a fuska kinji haushi idan yaga yana yimiki abu bakya damuwa haushi zekoma yanaji ki share hawayenki kinji Auntyna maganin kukana idan kina kuka ni kuma waye ze sharen nawa kukan inaso kiyimun wani alƙawari Aunty".
sosai kalaman Khadijah sukayi tasiri a zuciyar Inteesar ta share hawayenta tace"inajinki Khady".
"Aunty kiyimun alƙawarin duk inda kike zaki zama me ƙarfin zuciya bakomai zaki riƙa yiwa kuka ba koda ko ya cancanci hakan karkiyi agaban maƙiyinki".
wani murmushi ne ya suɓucewa Inteesar wanda har seda beauty point ɗinta suka bayyana tace"nayimiki my smalll sis insha Allah ".
"yauwa gwara da kika faɗamata Khady nima tintini nike bata wannan shawarar taƙiji".
nan sukaita hirarsu cike da nishaɗin bayan wani lokaci suka raka Hauwah har gida sannan suka dawo cikin farinciki suka nufi ɗakin Ummahnsu.

AFTER ONE WEEK
Abubuwa da yawa sun faru cikiko har da  soyayya me ƙarfi dake gudana a tsakanin Zaid da Inteesar wanda a yanzu basa iya cikakken 1hr ɗaya beji ɗaya ba ɓangaren Namijin duniya ko duk abinda yasan zeyi yaɓatawa Inteesar rai shiyikeyi dan yaga fishinta  bata taɓa nunamasa taji haushi  koda abu yaɓatamata rai sede ta nemi wani gurin inda tasan bame ganinta tasha kukanta domin ko bata tagaleshi ba shi seya tagaleta abu kaɗan zatayi yashiga lallatsemata ƙirji yace shine purnishment ɗinta ko kuma yashiga kissing ɗinta da sunan hukunci ɓangarenta da Zaid ko shirye-shiryen  biki Umminsa keyi ka'in da na'in domin Abbanshi yace bayason a wuce satinnan ba'ayi bikinba saboda yadda Zaid yabasu labarin yadda sukayi da Uwar Gwarama da alƙawarin da yayi na bayason bikin ya wuce sati ɗaya.

Zaune take a offuce ɗin Namijin duniya waya manne a kunnenta se zabga murmushi take tace"meyasa kake amsa na Hauwah ni nawa kace bakaso".
daga ɗaya ɓangaren Zaid yace"haba My 100% sure ɗina nina iya sakamiki suna se nine zakiji kunyar samamun suna ni meyasa banji kunyar canzamiki sunanba to nidai ki zaɓamun ".
yaƙarasa zancensa cike da shagwaɓa kamar wani ƙaramin yaro dariya tayi sosai sannan tace"to ɗan Ummih aikai namiji ne".
"au My 100% sure kina nufin mu maza bamu da kunya kenan".
zare sexy eyes ɗinta tayi kamar yana kallonta tace"nina isa faɗawa My Husband to be ɗina bashi da kunya".
cikin jindaɗin sunan data kirashi dashi yace"wow ɗan ƙara faɗa inji  amma sunan yamun daɗi sosai".

cikin shagwaɓar data riga ta zamemata jiki tace"bazan faɗaba nidai ba ruwana".
"hmm to naji da wanne sunan kika saka a number ta nima zan faɗamiki sunan dana saka akan number ki".
cikin shagwaɓaɓɓiyar murya ta maƙe kafaɗa kamar wata ƙaramar yarinya tace"naƙi wayon baseka faɗamun kowa ya riƙe nasa ".
dariya Zaid yayi tare da cewa"to ai shikenan tunda bazaki faɗaba ammm dama Ummih tace infaɗamiki ki sanar dasu Ummah gobe za'ah kawo lefe".
"tom zan sanar dasu insha Allah".
"yauwa anjuma zan shigo da yamma zankaiki ki gaida Ammi".
"toh Allah yakawoka".
"Ameen ya Allah I love you my 100% sure".
"love you more My husband to be".
cikin shauƙin juna sukayi sallama tana kashewa cikin zumuɗi tayi dialing no Hauwah tana ɗagawa tace"Hauwah yace gobe zasu kawo lefe".
cikin murna tace"masha Allah ,Allah yakaimu amma gaskiya basu kyauta manaba memakon yafaɗamana tun wuri musan snack ɗin da zamuyi amma se yanzu".
"wlh kuwa sannan kuma wai zezo anjuma muje mugaida Ammin su".
"toh Allah yakaimu".
"ameen ya Allah".
tana kashewa juyawar nan da zatayi sukayi ido huɗu da Namijin duniya ya zubamata narkakkun sexy eyes ɗinsa da alama ya daɗe tsaye kanta batama san yana na kallonta ba .

Cikin inda -inda tace"amm sir wani abun za'ah yimaka ne?".
saurin janye idanunsa yayi yawani basar kamar ba kallon ta yike ba jin ta anbaci lefe yasa lokaci ɗaya yaji lokaci ɗaya ransa yayi mugun ɓaci ga wani ƙullutun abu daya zo ya tsayamasa a maƙogoro ya rasa meke damunsa a zuciyarsa yaketa faman maimata kalmar"lefe badai lefanta za'ah kawo ba duka nawa take da iyayenta zasu yarda su aurar da ita amma kuma wanne shegen take faɗawa I love you".
wata zuciyar ce tace"mijin da zata aura take faɗawa tokai meye naka danta faɗawa masoyinta kalmar so ko sonta kakeyine".
wata zuciyar ce tace"Allah ya kyauta na na zauna ɓata lokaci gurin yin wata soyayya da wannan kwailar yarinyar never".
yana cikin wannan zancen zucin yaji siririyar muryarta aɗan daburce tace"amm sir kana buƙhatar wani abun ne?".
jin yadda tayi magana ne yasa tsigar jikinsa mugun tashi yayinda yaji wani irin yarrrrr tun daga ƙafarsa har tsakiyar kansa yayinda lokaci ɗaya yaji gindinsa ya miƙe saurin saka hannunwansa yayi a aljihu saboda kallo ɗaya zaka yimasa kaga yadda shatin gindinsa yadda ya jika wandon lokaci ɗaya yaji wata muguwar sha'awah ta dabaibayesa dakyar ya iya cewa"ki tafi theater hall yanzu".
"toh sir".
nanta fara tafiya tana juyamasa ɗuwawuka kamar wadda ke juyasu da gayya lokaci ɗaya yaji

wandonsa yayi mugun jiƙewa dakyar ya janye ƙafafunsa da suka yimasa nauyi ya nufi gurin drower ɗin da yike aje drugs ya ɓalla ya ɗauki ruwan gora ya kora zauna kan kujera yana mai maida numfashi 30mins sannan yaji yaɗanji sauƙi ya buɗe sexy eyes ɗinsa da suka ɗan ƙanƙance a zuciyarsa yace"meyike damuna ne wai kan wannan kwailar yarinyar da ko maganarta naji senaji hankalina yayi mugun tashi konama sha magani abanza".
wata zuciyar ce tace"ƙila sabon da kukayi ne yasa kakejin haka".
sauke ajiyar zuciya yayi tare da miƙewa ya ɗauki phones ɗinsa ya fita sakatariya Feenerh tashiga takemasa baya suka nufi hall ɗin daya kira meeting ɗin.

Yana shiga yaga ya zauna akusa da aminansa su Ahmad nan Adam ya miƙe tare da ɗaukar laudspeaker yace"salamu alakum".
amsawa jama'ah gurin sukayi da "wa'alaka salam".
"ba wani abu bane yasa muka taru ananba face daka yau munƙarawa duk wani ma'akaici dake ƙarƙashinmu albashi saboda yanayi da ake fama dashi na tsadar rayuwa wanda takai takawo ƙaramun ma'aikaci nauyi yayimasa yawa kuɗaɗen albashin da ake basu basu isa suyi hidimar iyalansu wannan dalilin yasa muka yanke hukuncin ƙarawa duk wani ma'aikaci albashi".
tafi hall ɗin ya ɗauka gabaki ɗaya da hayaniyar jin daɗi ta kauraye hall ɗin hakan yasa seda aka ɗauki 3mins kafin gurin yayi tsit Adam ya cigaba da cewa"sekuma abu na biyu kuma muna me farincikin sanar daku an kammala komai na babban branch ɗin pharmacy na Namijin duniya wanda za'ah cigaba da haɗa magunguna ranar asabar za'ah buɗesa in Allah yakaimu akwai a cikinku akwai wasu tsiraren mutane da muka ɗaukesu wanda matakin karatunsu ne yakaisu ba zaɓenmu ba zasu koma can da aiki ga sunayensu kamar haka zamu fara faɗowa tundaka sabbin canje-canje da aka samu ciki kuwa harda sakatarorinmu da aka canza su zamu fara kira".
tafi gurin yaƙara ɗauka da hayaniya.

Daɗa gyarawa Sakatariya Feenerh tayi ta kalli ƙawarta Zaby daketa ƙara shafa powder danta siye zuciyar Namijin duniya cikin kishi tace"mezan gani haka Zuby kike wani shafa powder sekace me ƙoƙarin yimun snatching".
cikin muryar riƙaƙun ƴan bariki Zuby tayi dariyar da iya kacinta fatar baki tace"haba ƙawata inani ina yiwa babbar aminiyata snatching ai Namijin duniya ni yafi ƙarfina wane ni dashi ai seku manyanmu inadai gyarawa ne domin ba'ah ga ƙawar Mrs Namijin duniya ba kamar wata mahaukaciya ba saboda banaso a rainamun ke ".
cikin jin daɗin kalaman Zuby tace"da wasa nike miki dama ƙawata nasan bazaki taɓa cin amanata ba aiko gwara ki gyara dakyau kinyi tinani mekyau kodon waccan berar da tin ɗazu suke kallonmu inkin gama ki bani nayi na gyara domin nasan ni za'ah fara kira da alama Oga fa kamar yafara kamuwa da soyayyata domin a sati biyunnan ni yike sawa inyimasa komai na office".

sosai ran Zuby yaɓaci da aminiyartata amma dake ƴar duniya ce seta dake kamar bataji komai ba  tace"masha Allah kice aiki dai yafara kyau ".
"sosaima kuwa".
 nanta  cigaba da abinda take tana gamawa ta miƙawa Feenerh powder tashiga shafawa .

Tin fara shafa powdernsu Feenerh Hauwah ta lura dariya shiga yi hakan yasa Inteesar kallonta cikin ƙasa da murya tace"lafiya kiketa dariya".
"wani abu ne yabani dariya mutanenki nagani anata aikin wahalar  da aka saba kallasu can ita da aminiyar nan tata".
taƙarasa zancenta tare da nunawa Inteesar su Feenerh dakyar tayi control ɗin dariyar data kusa suɓucemata  taita dariya ƙasa-ƙasa seda tayi me isarta ɗaga  idonnan da zatayi sukayi 4 eyes da Namijin duniya yana kallonta saurin janye lulu eyes ɗinta tayi domin gabanta dataji ya buga da ƙarfi  tashiga karanto duk addu'o'in da suka zo bakinta tace da Hauwah gaskiya iska na wahalar dame kayan kara mutum yayita abu a inda ba'ah san yanayiba".
"wallahi kuwa ni yanzu dariyama suke bani".
"nima haka dukkansu fa yadda na fahimta sonsa sukeyi amma da alamu ɗaya ke ha'intar ɗaya inda zasu dena saka wa'innan kayan da suke fitomusu da shegen ƙirjinnan nasu me kama da lawashin albasa  daya fimusu alheri ƙila ya kulasu ni banga abun so a wannan mutumi ba da mata suke zubar da ajinsu da darajarsu ta ɗiya mace suke cemasa suna sonsa yana ɗisgasu amma dukda haka suyita liƙemasa  yana yabasu ba".
"hmm wallahi kina bani dariya da ƙirjinnan nasu me kama da silifas da kike cewa mutuniyas ƙila fa harda ke a cikin wa'inda zasu koma pharmacy ɗin Namijin duniya ".
"hmm kema kinsan yadda mutuminnan ya tsaneni baze taɓa sakawa dani ba  wallahi  kima dena wannan tinanin ƙila dai kiga masu goga powder  a gaba-gaba".
Hauwah zatayi magana kenan sukaji muryar Adam a laudspeaker yana cewa"zamu fara da sakatariyar Namijin duniya mesuna Aisha Muhammad Ahmad ".
dammm gaban Inreesar yabayar sakamakon jin full name ɗinta dataji Adam ya anbata  basu ƙara tabbatar da abinda sukaji taji muryar Adam a laudspeaker yace"Malama Inteesar idan tana kusa zamu so ganinta a step tazo ta gabatar da kanta".
ƙululu taji cikinta yabayar cikin yanayin damuwa tace"Hauwah anyako ba wata kitumurmurar suka shiryamunba kuwa saboda mutanen nan basu da mutunci".
"ki kwantar da hankalinki Besty insha Allahh bakomai kedai kiyi addu'ar duk data zo bakinki kinji insha Allahu ba abinda zefaru se alkhairi basu isa suyimiki abinda Allah bemiki ba".
jiki a sanyaye tace "toh".
 jiki a sanyaye ta miƙe tafara tafiya yayinda  zuciyarta tashiga bugawa da sauri-sauri!!!!!!!!!

Votes and comments
Plz share to others

_*Daga Alƙalamun ƴar Mutanen Gwarzo.*_ ƴar Mutanen Gwarzo.*_🌻 *MAN OF THE WORLD* (NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

_Wannan shafin kyauta ne ga masoyan MAN OF THE WORLD a duk inda kuke Real eeshow na alfahari daku._

*BOOK 1*

*PAGES*2️⃣3️⃣➡️2️⃣4️⃣

Kamar kazar da kwai ya fashewa a ciki haka take tafiya domin idanun mutanen gurin gabaki ɗaya na kanta jiki a sanyaye taƙarasa step ɗin kanta a ƙasa ɓangaren Namijin duniya ko tunda ta fito ya kafeta da mayun idanunsa dake mugun bata tsoro harta tsaya a step ganin yadda tayi ƙasa da kanta ne yasa Namijin duniya taɓe baki a zuciyarsa yace"wai ita ala dole ace tanada kunya da tarbiyya".
a hankali ta ɗaga golden eyes ɗinta dake masifar tafiya da zukatan mutane taɗan saci kallon inda yike caraf suka haɗa ido gani tayi ya taɓe baki saurin janye idanunta tayi daga garesa zungurarsa Ahmad yayi yace"bakaga yadda mutuniyarka tayi bane dubeta a haka kamar mutuniyar kirki se rashin tarbiyya kala-kala a cikinta kamar kuɗin cizo batasan munkusa zuwa ƙarshen game ɗinba".
wani killer smile ya saki nan Adam ya cigaba da kiran sauran mutane ba sunan Feenerh ko ɗaya sede canzamata muƙami da akayi takoma sakatariyar Adam .

Ɓangaren Sakatariya Feenerh da Zuby ko mutuwar zaune sukayi ganin abubuwan da suke faruwa sosai ran Feenerh yakai ƙololuwar ɓaci tana huci ta zunguri Zuby da kamar zatayi kuka tace"nidai na rasa mena tsarewa wannan tsinanniyar yarinyar ne da bata da wani burin daya wuce taga bayana ƴar kujerar da nike taƙama da itama seda ta rabani da ita a tinanina da wannan kujerar yakamata nayi amfani gurin shawo kansa shine saboda ita tambaɗaɗɗiya ce tayimun haka dole wannan karon ta ɗanɗana kuɗarta domin sena nunamata na rigata zuwa duniya ko ta halin ƙaƙa senaga bayanta tsinanniya ƴar gidan masu dattin hula ƴar matsiyata ko

nawane a shirye nike dana  kashe matsawar zanga bayan wannan ƴar iska yarinyar".
"amma gaskiya kinyi sake wallahi Feenerh banyi zaton abun yayi ƙamari har haka ba aida nina ɗauki matakin dakaina amma ko yanzu bamu makaraba itaɗin banza duka yarinyar nawa take dako da ƙissa baki koreta ba saboda sakarci irin naki yanzu gashinan ta nunamiki ɗan hakin daka raina shike tsokalemaka ido domin koke kinƙi ɗaukar mataki akan wannan ƴar iskar yarinyar doleni naɗauka dan bazan taɓa barin wannan cin kashin data yimana ya tafi a banza ba wallahi".
taƙarasa zancenta cike da tsananin fusata hakan yasa Feenerh jin wani mugun sanyi a zuciyarta dan ita a tinaninta Zuby baƙaramin sonta take ba ganin yadda hankalin Zuby yayi mugun tashi hakan yasa  Feenerh cike da kulawa da sigar lallashi tace"ki kwantar da hankalinki ƙawata  muje gida muyi shawara da Ummah  muga ta inda za'ah ɓullowa al'amarin".
wani shu'umin murmushi taƙara yi tare da cewa"kidena ma tinanin zanƙi ɗaukar mataki akan duk wani abu da yike niyyar yimun shamaki da samun farincikina muradin zuciyata wanda nikejin kamar danni akayisa a shirye nike dana kauda duk wani abu dake niyyar nisantani dashi ko ƙanwata Zarah ce tayimun haka  wallahi senasa anɓatarmun da ita daka doron ƙasa domin a yadda nike jina yanzu haka na ƙuna bana tsoron ƙaure akan Namijin duniya banƙi inɓata da kowa ba".
cikin sigar kwarewa da harkar bariki Zuby ta ware ƙananun idanunta da suke kamar ankwantali duma tace"ƙawata kina nufin kenan zaki iya rabuwa dani".
"gaskiya Zuby baki da hankali kefa nacemiki ko iyayenane sena raba gari dasu bare wata ke  tin yaushe da zanmanta dake infara sabuwar rayuwa matsawar zan mallaki Man of the world da dukiyarsa".
sosai maganganun Feenerh suka ɓatawa Zuby rai dake ƴar bariki ce seta nunamata kamar bataji komai ba ta ƙaƙalo wani munafikin murmushi wanda iyakacinsa fatar bakinta tace"maida wuƙar aminiyata nima da wasa nike miki aini ko da baki kika nuna abu kinaso bazan taɓa son abunba  ko nawane abun ni me iya barmiki ce kinji tawan".
murmushin jindaɗi Feenerh tayi tace"godiya nike babbar aminiyata ".
wani shu'umin murmushi Zuby tayi wanda ita kaɗai tasan ma'anarsa suka cigaba da hira.

Ana tashi daga taron Inteesar ta nufi gurin Hauwah jiki a sanyaye tace"anyako Besty ba wani abun suke shirya ba kuwa mutuminnan ba alheri a tare dashi inaji a jikina kamar wata muguntar suka shiryamun".
"banaso Besty kina munanawa mutum zato banajin sun baki wannan muƙamin dansu tozar taki face sedan kin cancanta ki kwantar da hankalinki tawan ki cigaba da addu'ah ba wanda ya isa yayimaka abinda Allah bemaka ba".
"hakane kam Bestyna nagode sosai da kulawarki gareni Allah yabarmu tare".
"Ameen ya Allah muyi mu tafi mu shirya kar Uncle Zaid yazo yayita jiranmu".
"toh aiko kinsan shi sede ya jiramu badai mu jirasa ba bara naje na tambayesa koda abinda zan masa".
"ok hakan yanada kyau  nidai nariga da munyi sallama da Oga Ahmad bara injiraki a can".
taƙarasa zancenta ta maimata nuni da wata ƴar rumfar shaƙawata.
"toh".

nan kowaccensu ta tafi.

Bakinta ɗauke da sallama tashiga office ɗin jin shiru se ƙarar a.c daketa aiki yasata ɗagowa tashiga bin ko ina na office ɗin da kallo har lulu eyes ɗinta ya sauka kan wani tanƙamemen hofonsa sanye da wata haɗaɗɗiyar black arman suit sumar kansa tayi luf-luf da ita se ɗaukar ido take ya harɗe ƙafa ɗaya kan ɗaya bazato taji murmushin ya suɓucemata a hankali tashiga tafiya harta isa gurin ɗage tashiga yi ko hannunta zekai kan hoton dake hoton yaɗanyi sama sosai yasa dukda ɗagen datayi hannunta bekai ba shiru tayi harta juya sekuma ta fasa ta nufi gurin wata haɗaɗɗiyar resting chair ɗinsa me tayoyi ta turata daidai saitin photon ta tuɓe takalminta ta taka tsayinta yayi daidai da tanƙamemen photon lallausan hannunta tasa tashafa hoton cikin wani irin yanayin da batasan kona menene ba takai bakinta daidai saitin bakinsa tasakarmasa wani hort kiss tasaki wani sansanyan murmushi tare da ƙara kai lallausan hannunta kan photon daidai saitin hancinsa tace"sturborn kaidai baka da girma ko kaɗan sena jikinka".
taƙarasa zancenta tana mai ƙara sakarmasa wani hort kiss zata janye bakinta daga jikin photon kenan taji lion voice ɗinsa ta daki dodon kunnenta yace"inkin gama kiss ɗin kya iya sakkowa anga ɗan sangiri saurayi ba kamar ƙolon saurayinki ba ".
a ruɗe ta juya jiki na rawa zata sakko hakan yasa kujerar da take ta tafi zuuu zata faɗi sauri rife golden eyes ɗinta tayi domin tagama sadaƙarwa da zata faɗi tajita a jikin mutum ƙamshin turarensa ne ya tabbatar mata da shine a hankali tashiga buɗe oily eyes ɗinta ta saukesu kan kyakyawar fuskarsa kallon-kallo suka shiga yi na tsawon 5mins yayinda iskar damuna tashiga kaɗawa hakan yasa gabaki ɗayansu suka tsunduma cikin duniyar tinani buɗo ƙofar da akayi ne yasasu dawowa daga duniyar tinanin da suka shiga ganinsu a haka yasa ran Meemah yayi mugun ɓaci .

Ɓangaren Namijin duniya ko kallo ɗaya yayiwa Meemah data banko musu ƙofa ya ɗauke kansa jin Inteesar nata mutsu-mutsun ya sauketa yasashi ƙara matseta a faffaɗan ƙirjinsa gefe guda kuma cike da muguntа ya takemata ƙafa da haɗaɗɗen takalminsa sosai taji azabar yadda ya takemata ƙafa amma hakan be hanata mamakin abinda yikemata ba a zuciyarta tace"anyako wannan mutumin kanshi ɗaya kuwa".
lokaci ɗaya bugun zuciyarsa su yaƙaru saboda yadda ƙirjinsu ya haɗe guri ɗaya tana cikin zancen zuci taji muryarsa cikin wani shegen salo da batasan yanada shiba yace"sannu My Angel kiriƙa yimun a hankali da jikinki kinsan banaso kina wahalarmun da kanki saboda keɗin rayuwata ce badon nazo a lokacin daya dace ba daya kike tinanin za'ayi".
yaƙarasa zancensa tare da kashemata sexy eyes ɗinsa baki buɗe Inteesar ke kallonsa fuskar ɗauke da tsananin mamaki ganin yadda tayine yasashi gyaramata zama a ƙirjinsa yashiga caring ɗinta kamar kwai yayinda gefe guda kuma yaketa mitsitsikemata ƙafa ɓangaren Inteesar ko ba abinda take se al'ajabin abinda yike mata.

Ganin ƙofa a buɗe bakowa ne yasa Zuby cewa"yauwa Feenerh mushiga kawai ki basa haƙuri in wani abun kika yimasa yayi haƙuri ya maida ke muƙamunki ina ganin hakan zefi kuma a ganina wannan shine stage na farko da yakamata mubi domin se muna haɗawa da ƙissa Allah ma ya temakemu wannan makirar yarinyar bata nan komai zezomana da sauƙi".
"mu wuce kawai gobe na shawo kwalliya speacial domin bashi haƙuri".
cike da zaƙuwa Zuby tace"a'ah muje yanzu".
"toh tunda kin matsa mushiga ɗin".
Feenerh taƙarasa zancenta suna shigewa cikin office ɗin sandarewa suka yi sakamakon ganin Namijin duniya rungume da Inteesar yana caring ɗinta itakuma tayi luf a faffaɗan ƙirjinsa kamar wata ƴar baby yayinda daka ƙasa kuma yake ƙara mutsitsike mata ƙafa.

Ɓangaren Namijin duniya ko yi yayi kamar besan da mutane a gurin ba hakan baƙaramun ƙara ɓatawa su Meemah da sukayi mutuwar tsaye rai yayi ba shiko ɗan gogan cigaba yayi da caring ɗin abarsa kamar wata matarsa saurin yin baya su Feenerh sukayi cikin tsananin ɓacin rai yayinda Meemah ma tabi bayansu zuciyarta na tafarfasa ta buga musu ƙofa da ƙarfi .

Mutsu-mutsu takeyi cike da tsananin ɓacin ran abinda yayimata a gaban mutane yayinda wasu hawaye suka shiga sintiri a kumatunta a zuciyarta tashiga tinanin wanne irin kallo mutanen nan zasu yimata ƙin sakinta yayi hakan yasa ta ƙara lafewa a ƙirjinsa wani ƙasaitaccen murmushi ya saki ganin yadda ta sakankance taƙara lafewa a jikinsa hakan yasa cike da mugunta ya hankaɗata ta faɗi ƙasa jikake ƙass ƙarar kashin ƙafarta yayi ƙara yayinda lokaci ɗaya ƙafar ta kaure da zugi ga tsamin da tayi cikin yanayi na jin zafi tace"ochhhhhh".
murmushin mugunta a gadarance yace"matsamun da wannan ƙazamun jikin naki dayasha taɓawar ƴan bariki kin wani lefe jikin mutum kina yin pretending kamar wata ta Allah bayan kuma a zuci ba haka bane kina wani kakkare jiki kamar wata uwar mata mezan gani abu kamar kwan kurciya".
yaƙarasa zancensa tare da ƙara shan mur kamar bashi yayi maganar ba ya wani ƙara haɗe rai ɗaga idonnan da zeyi sukayi ido huɗu da!!!!!!!!!

*Sorry my fans kuyi haƙurin da rashin typing yafaru ne saboda wani uzuri daya tasomun me ƙarfi amma yanzu na dawo normal zamu fara wasa kullum insha Allahu zaku fara samu update sau ɗaya ko biyu a rana matsawar zaku bani haɗin kai ta hanyar suburbuɗamun comments and votes zaku sha mamaki domin yanzu zan tsoma hannu cikin labarin dan shimfiɗa mukayi

yanzu zamu fara wasan.*

Votes and Comments
Plz share to others

_*Daga Alƙalamu🌻 *MAN OF THE WORLD*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

*BOOK 1*

*PAGES* 2️⃣5️⃣➡️2️⃣6️⃣

Dasu Ahmad da sun daɗe suna kallon ikon Allah abinka da miskilin mutum se ya wani basar kamar besan abinda ke faruwa ba ya wuce ya zauna a kujerar office ɗinsa yashiga duba takardun dake aje akan table ɗinsa jawo system ɗinsa dake gefe guda yashiga operating juyawa su Adam sukayi cikin sauri ɗinta ɓangaren Inteesar ko kasa motsi tayi saboda tsananin azabar da ƙafar kemata lokaci ɗaya hawaye suka wankemata fuska cikin office ɗin ba abinda kakeji se shashekar kukanta ɓangaren Namijin duniya ko jin kukanta yike har cikin ransa ya rasa dalili a zahiri seka ɗauka wani mahimmin aiki yikeyi a system ɗinsa a cikin zuciyarsa ko jin wani irin abu yakeji dangane da kukan da takeyi .

Jiyayi duk be kyautaba abinda yayimata zuciyarsa ce tashiga rayamasa idan Rahamansa wani yayiwa haka zeji daɗi zuciyarsa ce tabashi amsa da"a'ah ".
wata zuciyar ce tace"to ita meyasa kake yimata haka?".
wata zuciyar ce tace"ka rabu da ita ai rashin kunyarta ce ta jamata cigaba da aikinka kawai".

yana cikin wannan zancen zucin yaji sallamar su Ahmad ba tare daya ɗago ya kallesu ba yace"wa'alakumus salam".
yaƙarasa amsa musu tare da duba wani file dake gabansa kamar da gaske ya wani ƙara haɗe rai dan karsu yimasa magana ganin haka yasa suma basu bi takansa ba suka nufi inda Inteesar take cikin nuna basu ga duk abunda yafaru ba Adam yace"subahanallah Aishatu meya samu ƙafar taki haka naga ta kumbura Abdallah meyafaru da ita haka".
ba tare daya ɗago daga danna system ɗin da yike ba kamar wanda yake wani abu me mahimmanci yace"ka tambayeta man nima yadda kaganta haka na ganta".
saurin juyawa Adam yayi gun Inteesar cike da takaicin amsar rainin hankalin da abokinsu ya bashi karo na farko a rayuwarsu da sukaji tausayinta cikin tausayin halin da take ciki Adam yace"meyasameki Aishatu ".
cikin siriryar muryarta dake nuni da tasha kuka tace"gurɗewa nayi Sir".
taƙarasa zancenta kuka na niyyar cin ƙarfinta yayinda takejin wata muguwar tsanarsa na ratsa zuciyarta ganin shi yajimata ciwo amma shi ko ajikinsa sosai tabasu tausayi cikin sigar lallashi Ahmad yace"sannu kinji bara na kira Hauwah ta temakamiki semu kaiki asibiti naga ƙafar ta kumbura sosai".
cikin sanyin murya tace"toh Sir nagode".
"bakomai".
nan yashiga dialing number Hauwah bugu ɗaya ta ɗauka cikin girmamawa tace"salamu Alaikum".
"wa'alaiki salam ki sameni a office ɗin Abdallah".
"toh sir".
nan ya kashe ko minti goma ba'ah yiba Hauwah tayi knocking buɗemata Adam yayi haɗe da cewa"temaka mata kisamun ita a mota mukaita asibiti naga ƙafar ƙara kumbura takeyi".
yaƙarasa zancensa yana mata nuni da inda Inteesar ke yashe se lokacin ta lura da Inteesar daketa faman kuka cikin tashin hankali ta nufi gunta tana cewa"meya sameki Besty".
kasa magana Inteesar tayi kuka ya kuɓucemata se nuni takemata da ƙafarta sosai Hauwah taji tausayin halin da aminiyarta take ciki tashiga ƙoƙarin temaka mata .

Kasa ɗagata tayi hakan yasa Ahmad nufar gurin yana cewa"bara na temaka miki".
be ƙarasa zancensa ba yaji Namijin duniya ya bangajesa ransa a mugun ɓace yayinda yaketa faman huci yace"muharramarka ce da zaka taɓatamata jiki meye alaƙarka da ita ?".
cikin tsananin ɓacin rai ya nufi gurin da Inteesar take yashe tana kuka wani guntun tsaki yayi sannan yasa lallausan hannunsa ya ɗauke ta cak kamar wata baby ya wuce fuuu baki sake suke kallonsa har ya ɓacewa ganinsu sauke numfashi gabaki ɗaya sukayi Adam ya kalli Ahamad suka saki wani shu'umin murmushi wanda su kaɗai sukasan ma'anarsa Ahmad ya kalli Hauwah gani yayi duk tashiga damuwa yace"ki kwantar da hankalinki ba abinda zemata nasan asibiti zekaita kya iya tafiya gida nasan shima idan sun dawo kaita zeyi".
"toh Sir".
nanta fice tabarsu ba abinda sukeyi se aikin murmushi.

Ɓangaren Namijin duniya ko yana fita ya nufi gurin haɗaɗiyar Bugatti ɗinsa sabuwa dal da ita kafin yaƙarasa securities ɗinsa sun buɗemasa motar back seat ya ajeta jin yadda take kukane yasashi sakin wani dogon tsuka ya juya ya nufi gurin driver security ɗin dake niyar shiga mazaunin driver ya dakatar da hannu yace"nizanja ku zauna ku".
"okay sir".
nan security ɗin ya matsa ya shiga harya fara tada motar sekuma ya kashe yayi tsaki ya fita ya zagaya inda take yasa lallausan hannunsa ya ɗauketa cak ya buɗe gefan me zaman banza yasata ya zaga yashiga mazaunin driver  yaja motar da  gudu ya cilla hancin motarsa titi shiru ne ya biyo a tsakaninsu kowanne da abinda yike saƙawa a cikin zuciyarsa ita tana tinanin itako meta tsarewa wannan mutumin dahar ya tsaneta haka shikuma yanajin duk beji daɗiba ganin yadda tayi ƙasa da kanta tana shashekar kuka ta wutsiyar ido ya saci kallonta gani yayi tana nan  dai a yadda take sosai tabasa tausayi amma dake miskilin gaskene se ya nuna be damu da halin da take cikiba sema taɓe baki da yariƙa yi a haka har suka isa wani tanƙamemen  na masu faɗa aji a ƙasa me suna A2 bakin tanƙamemen parking space ɗin hospital ɗin yayi parking tare da juyar da kansa ya kalleta tana nan a yadda  take tsaki yayi ya buɗe mota ya zagaya inda take ya ɗauketa kamar wata baby yayinda ƴan hospital ɗin se bashi respect suke ya nufi wani room da ita yana shiga haɗaɗɗen room ɗin ya kwantar da ita akan wani haɗaɗɗen sick bed wanda inkana kai seka ɗauka na  gidane gidanma wanda ya amsa sunansa gida mamakine ya kamata seta make gefe guda kuma wani mahaukacin tsoro ne ya dirarmata ganin irin aljannar duniyar gurin da take yana nan tsaye kanta sega wani Doctor yashigo bayan sun gaisa yayimasa bayani abinda ya sameta amma becemasa shiya jimata ba nan yashiga bata emergency care domin ƙafar ta kumbura sosai.

*FEENER POV*

Suna fitowa daka Office ɗin Namijin duniya Zuby ta dafe shafaffen ƙirjinta tare da kallon Feenerh cikin tsananin baƙin ciki tace!!!!!!!!!

Votes and Comments
Plz share to others

_*Daga Alƙalamun ƴar Mutanen Gwarzo.*_n ƴar Mutanen Gwarzo.*_🌻 *MAN OF THE WORLD*

(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

*BOOK 1*

*PAGES* 2️⃣7️⃣➡️2️⃣8️⃣

"Gaskiya wannan tsinanniyar yarinyar anyi tambaɗaɗiya daka gani sede in gurin boka taje banda haka banga abinda Namijin duniya ze kalla a jikinta ba bare har yayi sha'awar aurenta muna ganinta  saida kaji saida kaji ashe har shanu ma siyarwa take".
"aina faɗamiki dama ƴar iskar yarinyar nan ta wuce duk inda kike tinani domin ba Allah a tare da ita dakanan direct mu wuce gidan Ummah mu tafi gurin Boka".
"aiko dai kema kince wani abu domin abunnan gagarumi ne".
"eh mana hatsabibiya ce yarinyar ga kuɗin dana ciro zankai gidan adashi mutafi dasu kawai gobe na ciri wasu inkai".
"toh muje ammafa yarinyar nan koda ansamu anɓan bareta daka jikinsa aciki wasa tunda ita yafara runguma kafinke amma dai nima zaki bani passentage ɗina daiko".
"gaakiya baki da haƙuri Zuby kinsan dai ai zanbaki ungoni".
"ai gaskiya ce najiɗin bani da haƙurin indai akan kuɗine gwara kibani haƙƙina".
a zuciye Feenerh ta dankawa Zuby kuɗin tace"gashinan sarkin zalama".
"naji ɗin kome zaki ce kice ɗin ina ganin kawai mu kira Ummah ta fito titi mu ɗauketa mu wuce kawai ina ganin tafiyar zata fimana sauri".
"ok kirata da hanzari dan Allah".
kamar yadda Zuby tace hakan sukayi suka kira Umman Zuby suna isa bakin layinsu suka ɗauketa suka tafi.

"Ummah gaskiya ni nagaji da wannan ƙailular taki kinsanko irin san da nikewa mejan kunnenan kuwa da kika wani ƙi maida hankali kan zancen".
"kefa Jameelah daɗina dake rashin haƙuri ki kwantar da hsnkalinki indai ina numfashi baki da wani mijin se mejan kunne domin yau ko gobe zansa Malam yasa Zaidu mejan kunne yazo gaidashi semu samu kafar saka maganin boka Tsula kai waye nafiki son kiyi aure gidan daula

kodon inriƙa zuwa inaɗan yago abinkaiwa a bakin salati".
"yanzu naji duka ".
"kedai abinda nike so dake kiɗanje ki wankemun ɗan wanke-waken can domin yau waccan tsinanniyar yarinyar batayiba ta tafi yawon tazubar ɗinta".
ƙin tashi tayi dakyar ta tashi tana zumɓure-zumɓuren baki ta fita.

Ɓangaren Namijin duniya ko Doctor na gama gyarawa Inteesar ƙafa cikin yanayin caring Doctor Shahid yace"princess gaskiya kinada dauriya da watace da yanzu tana nan ta cika ɗakinnan da ɓararrako".
wani sansanyan murmushi Inteesar tayimasa wanda yayi mugun tafiya da zuciyar Doctor Shahid tace"nagode".
"ba godiya a tsakanin princess kedai kawai ki kula da shan maganinki insha Allahu nanda kwana uku zakiji ƙafar ta saki".
yaƙarasa zancensa yana sakarmata wani shu'umin murmushi ,murmushin itama ta mayarmasa itama cikin siriyar muryarta dake tafiya da zuciyar ɗa namiji tace"insha Allah zankiyaye".
wani ƙullutun baƙin cikinsu ne ya tokarewa Namijin duniya maƙogoro ganin yadda Inteesar keyiwa Doctor Shahid murmushi tsaki yayi a karo na uku sakamakon jin Doctor Shahid na niyyar ƙara jan Inteesar da hira murya aɗan daƙile cikin basarwa ya katse Doctor Shahid tare da cewa" Mallam kayi abinda ke gabanka".
"sorry Sir".
nan Doctor Shahid ya tsuke bakinsa saboda yana ɗagowa yaga Namijin duniya na jifansa da kallon kashiga taitayinka beƙara cewa da Inteesar komai ba ,ɓangaren Inteesar ko wani ƙullutun baƙin cikinsa taji tashiga itako metayiwa wannan mutumin da bayason yaga wani ya raɓeta bayason yaga wani yana nunamata kulawa tana farinciki tana cikin tinani taji muryarsa a ɗan daƙile yana cewa da Doctor"thanks".
saurin dawowa tayi daga duniyar tinanin data tafi taji ƙamshinsa a gabda ita waigawa tayi taganshi befi saura taku biyu ya iso inda take ba saurin miƙewa tayi dukda zafin da ƙafarta kemata ta haɗe girar sama data ƙasa dan karya kaimata wargi tashiga aikamasa da harar wutsiyar ido tafara tafiya tana ɗingishi murmushin gefan baki yayi ganin yadda ta wani haɗe rai yabi bayanta yarigata zuwa gurin mota hakan yasashi yana isa ya buɗemata murfin motar har tayi niyyar wucewawarta taga idanun mutanen gurin gabaki ɗaya yadawo kansu hakan gefe guda kuma wata zuciyar tace mata"kishiga har yanzu kina ƙarƙashin ikonsa tunda baku tashi daka gurin aikiba".
hakan yasata jiki a sanyaye ta shiga ya mayar ya rife ya zaga yashiga mazaunin driver yaja motar suka bar gurin yana fita daka get ɗin gurin ya cilla hancin motarsa titi ya ware a.c ɗin dake motar ya kunna karatun Alqur'ani megirma ƙira'ar Sudais tashiga tashi a cikin motar suratul Muhammad ba tare daya ƙara bi takanta ba yashiga bin ƙira'ar da daddaɗar muryarsa me daɗin sauraro .

Ɓangaren Inteesar ko juyar da kanta tayi tana kallon titi hakan datayine yabashi damar ƙarewa

fuskarta kallo ɗan motsawa tayi hakan yasashi saurin  ɗauke kansa daga gareta cikin nutsuwa yake tuƙi ganin hankalinsa ya karkata akan tuƙin  taga ya nufi hanyar cikin gari da ita saurin kallonsa tayi gani tayi ya wani make kamar besan metake  nufiba sosai ranta yakai ƙololuwar ɓaci da abubuwan da yikemata ta aro jarumta cikin tsiwa tace"Malam ajeni anan".
yi yayi kamar badashi take ba hakan daya yimata baƙaramin ƙara tunzurata yayiba a harzuƙe tace"Malam ka ajeni anan".
ƙara banza da ita yayi hakan yasa takai hannu cikin ɓacin rai zata murɗa handle ɗin motar kafin taƙarasa taji ƙarar sa lock ɗinsa hakan yasa ta koma ta zauna tare da jingina da  jikin kujerar ta lumshe oily eyes ɗinta cikin kwanciyar hankali ya cigaba da tafiyarsa  harya isa wani tanƙamemen mall   mesuna  MAN OF THE WORLD SHOPPING MALL da manyan baƙi ƙarasa shiga gurin yayi tare da yin parking a tanƙamemen parking space ɗin gurin   yana daidaita parking ɗinsa yaɗan saci kallonta gani yayi har bacci ya ɗauketa a haka jiyayi wani murmushin dabe shirya yinsa ba ya kuɓucemasa ganin yadda ta duƙunƙune ne yasashi gane a.c tayimata yawa yaɗan ragemata haɗe da kwantar mata da kujerar ya gyaramata kwanciyarta ya buɗe ya fita tare dasa lock ta waje ya nufi cikin gurin bejima da shiga ba yafito bayansa da masu aiki a gurin sanye da riguna da kaya niƙi-niƙi a bayansa  danna key ɗin motar yayi har zasu zuba a boot ya  dakatar dasu  yayimusu nuni da  gidan baya cikin girmamawa suka zuba yashiga motar yaja seda sukayi tafiya me nisa rasa hanyar dazebi yakaita gidane yasashi juyawa ya kalli inda take gani yayi ta tashi taɓe baki yayi haɗe da cewa"ina  zankaiki".
ba tare data kalli inda yike ba tace"Suleja amma a titi zan sauka".
ba tare daya tankamata ba ya juyar da kansa ya cigaba da tuƙinsa cikin kwanciyar hankali yaƙara volume yashiga bin karatun Alqur'ani taɓe baki tayi a zuciyarta tace"ashe su wa'eeh an iya abun mutane".
jin muryarsa tayi kamar a mafarki yace"keeeh dawa kike".
se lokacin tagane a fili tayi maganar tsuke bakinta tayi har suka isa bakin titi kamar yadda tace dashi yayi parking gefan  titi ba tare daya kalleta ba yasa hannu ya jawo ɗaya daka cikin ledojin da yasa aka saka a baya ya buɗa ya fito da wasu rantsatsun abayas masu ɗaukar hankali ya zaro ɗaya daga ciki ya buɗa ba tare daya kalleta ba yace"daka yau wa'innan kayan zaki riƙa sawa da safarsu da niƙab ɗinsu dan bazan lamunci saka wannan banzan gyalen da kikeyi ba domin Comphany ɗina ba gurin nanaye bane da mutum zaki riƙa saka wa'innan fugaggun gyaluluwan naki masu kama da matacin koko  a ciki akwai hijabs kowanne kowanne kaya da kalar niƙab ɗinsa da hijab ɗinsa  su zaki riƙa sawa".
wata dariyar rainin hankali tayimasa tare da taɓe baki ta aro jarumta tace"waikai meyasa kake son takurawa rayuwata ne sekace wani mijina ina ruwanka da kayana  kuma da kake cewa gyalena kamar matacin koko meye naka a ciki naga tundaka gidanmu nasawo kayana  meyasa su basu yimun maganaba sekai  kuma kai bakaga irin shigar da Sakatariyarka  take ba se tawa saboda ni kaɗai ka tsana to bazan dena sawa ba  banason kayan kakaiwa matarka tasa domin ni a ganina ita zakaiwa wannan kullen baniba".
taƙarasa zancensa  tare da ture rigar daka jikinta cikin isa yace"ke wacece da zanyimiki kyauta ki mayarmu dame kike taƙama baki isa kin karyamun record ba  dole ki ansa".
wani kallon tara saura kwata tayimasa cikin tsiwa tace"mutum ce kamarka kai waye da baza'ah mayarmaka ba  masha Allah kaga seka aje record akaina anyi rejecting ɗin kyautarka domin ni wallahu bazan ansa ba ka adana zasu yimaka amfani gun matarka".

taƙarasa zancen tare da saurin murɗa handle ɗin ƙofar cikin sa'ah tajishi a buɗe tayi  saurin fita ganin ya kawo hannunsa da niyyar cafkota tafice cikin sauri dukda tanajin zafin ciwon da ƙafarta ke mata karo na farko a rayuwarshi daya yi murmushi dukda rashin kunyar data  tayimasa  beja motar ba har seda yaga ta tsallaka titi tahau napep sannan ya tada motarsa yabar gurin a guje.

8:30pm
Tsaye yake a ƙofar gidansu yanata dialing number ta amma amsar ɗaya switch off sosai hankalinsa yayi mugun tashi ɗaga kannan da zeyi yaga Hauwah  ta fito daka gidansu tunkaro inda yike tsaye sosai yaji wani irin sanyi ya ziyarci zuciyarsa bakinta ɗauke da sallama taƙarasa murmushin daya ƙara masa kyau yayimata cikin girmamawa Hauwah tace"Uncle Zaid anyini lafiya".
"inafa lafiya banji zuciyata ba ina zakijini naga ta lafiya".
sosai  Hauwah daɗin kalamansa akan ƙawarta nanta labartamasa duk abinda yafaru a iya yadda tasani sosai hankalinsa ya tashi sosai takejin daɗin yadda yake caring ɗin ƙawarta tace "Uncle ka kwantar da hankalinka bara inshiga insanar musu seka shiga ka ga jikinta".
"aiko da kin temakeni domin bakiji yadda hankalina yayi mugun tashiba dukda kin faɗamun amma hankalina yaƙi kwanciya in naganta hankalina yafi kwanciya".
"tom bara naje".
nanta shiga .

A tsakar gida tasamu Abbah da Uwar Gwarama zaune Abbah yana cin tuwo Uwar Gwarama tana ƙuƙula magungunan mata da take siyarwa abinka dame sana'ah goma maganin me gasa ƙarasawa tayi inda suke cikin girmamawa tace"Abbah sannunku da hutawa".
"yauwa Hauwah ya mutanen gidan naku".
"lafiya ƙlau Abbah dama Zaid ne yazo zamuje gidansu shine nike faɗamasa Inteesar ɗin batada lafiya ……".
bata ƙarasa abinda take son cewa ba  cikin zalama Abbah ya tari numfashinta da cewa "meyasa to baki ce yashigo ciki yagaida itaba aida kince ya shigo aishima yanzu yazama ɗan gida ko Tsahare".
tsilum Uwar gwarama tace"aiko dai Malam".
jin abinda Uwar Gwarama tace sosai yabawa Hauwah mamaki tace"ai Abbah nacemasa bara inyimasa iso yashigo".
"toh! toh!! toh!!! kin kyauta  ki sanar dasu suɗan gyatta  seki shigo dashi".
"toh".
nanta nufi ɗakinsu Inteesar  zaune tasamesu Khadijat na karantawa Inteesar wani littafin Real eeshow mesuna ZANJIRATA sosai suke jin daɗin littafin domin yana kaimusu Umman su kuma tana kan sallaya tana lazumi hararsu Hauwah tayi tace"yanzu nan saboda rashin mutunci shine kuka cigaba da karantawa koku kirani inason jin yadda zata kaya tsakanin Amatujjabar da Yayah Mahmud saboda dramar su nakaimun ".

"ya haƙuri Aunty Hauwah zan karantamiki kema seda nace tabari kizo taƙi kinsan Aunty da gauƙa yanzu ma kuma muka fara".
"toh ƴar ƙanwata takaina ".
taƙarasa zamcenta ta nufar gurin Ummah duƙawa tayi ta sanar da ita zuwan Zaid sannan tasa suka ɗan kintsa dukda ɗakinsu fes-fes yike basu da lalaci nanta fita tashigo dashi.

Uwar Gwarama na ganin fitar Hauwah ta kalli Abbah daketa sukurkuta lomar tuwo yana santi tace"Malam bara inɗanje inɗan kunna turaren wuta sirikinmu bayazo yanaɗan jin bashi -bashi ba kadai sanni da iya karramar baƙo bare kuma babban sirikinmu".
"aiko dai da kin kyauta".
wani shu'umin murmushi tayi ta wuce ɗakinta tana shiga ta iske Jameelah tana waya da saurayinta cikin azama tace"ke banza kina nan kina shashsnci Allah yakawo mana dama Zaidu yanzu ze shigo ya duba waccan tsinau ɗin ki tashi ki ɗebo rushi kizuba magain nan".
tsalle Jamilah ta buga tare da miƙewa cikin jin daɗi tace"I love you Mamah na maganin kukana".
ta fice cikin sauri murmushi Uwar Gwarama tayi ta tafi ta ɗakko maganin da boka yabata ta fito waje a tsakar gida suka haɗu da Jameelah ta ebo wuta a marfin langa nanta jiki na rawa ansa Uwar Gwarama tayi tana murmushi tace"yimaza kije kiɗan kintsa jikinki karya ganki kamar wata ƴar jaka".
"toh".
nanta wuce ita kuma ta buɗe maganin ta zuba .

Zaid na shigowa ƙamshin turarennan ya bugu hancinsa lokaci ɗaya yaji kansa yashiga saramasa dakyar yake iya ɗaga ƙafa yake tafiya har suka isa!!!!!!!!

Votes and Comments
Plz share to others

_*Daga Alƙalamun 🌻 *MAN OF THE WORLD*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK 1*

*PAGES* 2️⃣9️⃣➡️3️⃣0️⃣

Inda Abbah ke zaune yaƙarasa tare da zama kan sallayar da aka shimfiɗamasa ya zauna cikin girmamawa yace"Abbah ina yini".
"lafiya ƙlau ya wajen iyayen naka".
"lafiya ƙlau Abbah suncema suna gaisheku".
"masha Allah Hauwah yimasa jagora zuwa gurin mejikin".
"toh Abbah".
taƙarasa faɗa tana kallon Zaid da bashi da niyyar miƙewa ɓangaren Zaid ko ji yayi  duk bayako son ganinta daurewa yayi ya miƙe da nufin bin bayasan sukaji muryar Uwar Gwarama dake fitowa daka ɗaki cikin shiga ta alfarma jiki na rawa Zaid yayi saurin duƙawa yace"Ummah ina yini".
ganin yadda jikinsa yaketa faman tsuma baƙaramun daɗi taji ba a zuciyarta tace"kai gaskiya Boka Tsula aikinka na kyau jibi yadda jikin wannan shu'umin yaron daya wulaƙantani yaketa faman karkarwa kamar mazari kaɗanma kagani ɗan shegiya zaka kwashi kashinka a hannu domin seka gane shayi ruwa ne seka zama tamkar raƙumi da akala domin Jameelah se yanda tayi dakai badai kai ƙaramin tsageraba hadda wani cewa dani ni Inteesar nike itakuma har wani gwalli takeyi wai ita zatayi aure gidan jindaɗi maga yadda za'ayi ayi auren matsawar ina numfashi bazan taɓa barin ɗiyar Aminah taji daɗin duniya ba kamar yadda na hanasu jin daɗin gidannan haka bazan taɓa barinku kuji daɗin gidan mijiba sede ku ƙare a bauta matsawar ina numfashi ".
katsemata zancen zucin da takeyi Zaid yayi murya na rawa yakuma cewa"Ummah ina yini".
wani gauron numfashi ta sauke haɗe da dawowa daga duniyar tinanin data lula tace"lafiya ƙlau yaron kirki ya wajen magabatan naka".
baki har ɓari yikeyi yace"lafiya ƙlau Ummah sunama gaisheku",.
a wani yatsune Uwar Gwarama tace"muna amsawa ɗiyar kirki ƴan makaranta kifito ga yayanku yazo ku gaisa ko duk hadda ce har yanzu kiriƙa barin kwakwalwarki ta huta dan Allah darenma ace mutum baze hutaba sekace al'huda-al'huda aikya fito ku gaisa inyaso seki koma kicigaba da karatun".
Jameelah dake ɗaki tana chart ɗinta da saurayinta ce tayi gyaran murya alamun bata kai ayaba ta cigaba da danna wayarta bayan 5mins  cikin fi'ili tayi kabbara sannan ta miƙe taƙara feshe ko ina na jikinta da turare sannan ta gyara zaman hijab ɗinta tashiga tafiya cikin yanayin ɗaukat hankali.

Ganin yadda jikin Zaid keta faman ɓari baƙaramun mamaki  hakan yaba Hauwah ganin yadda bakinsa har rawa yike gurin gaida Uwar Gwarama tinani tashiga yi a zuciyarta tashiga tinanin ita a iya saninta Zaid baya shiri da Uwar Gwarama to kuma meyasa taga jikinsa har ɓari yikeyi kanta rasa wanda zebaa amsa ne yasata tsuke bakinta tana mamakin iyayi irin na Uwar Gwaramaa zuciyarta tace"hmmm iska na wahal dame kayam kara ko a ina Jameelah ta taɓa shiga class oho Allah dai yasa ba wata kitumurmurar suka haɗa ba".
tana cikin wannan zancen zucin taji ƙamshin turaren Jameelah ya bigi hancinta saurin ɗagowa tayi caraf sukayi ido huɗu da Jameelah daketa faman zuba ƙamshi tasha kwalliya kamar wadda zata gasar kyau baƙaramun ɗaurewa kanta yaƙara yiba da mamakin abinda take gani ganin abun take kamar almara wata uwar harara Jameelah ta bankamata  suna haɗa ido da Zaid tasakarmasa da wani narkakken murmushi wanda yasashi suman wucin gadi lokaci ɗaya yaji wani mugun sonta na fisgarsa jiyike duk duniya bashida wani  abu da yikeso kamarta martanin murmushin data yimasa ya mayarmata wani sanyine ya ratsa zuciyarta inda takejin wata muguwar ƙaunarshi na ƙara ninkuwa a cikin zuciyarta jitake kamar taje ta rungumesa haka takeji  .

Uwar Gwarama ce ta kalli Zaid cikin  iyayi tace"kaganta nan Zaidu kullum aikin kenan daka hadda se zuwa  makaranta koda yike tafi  masu rataya jaka kullum  kamar wanzamai  aje can aje nan  duk wani lungu na garinnan inkabi seka gansu kamar wa'inda akaimusu hakika da kare shiyasa ƙilama shiyasa aka rasa mashinshini".
murmushi Zaid yayi yace"masha Allah sister  yanzu izunki nawa".
farr Jameelah tayi da mitsi-mitsin idanunta da suka ƙara narkar da Zaid cikin ƙaunarta zatayi magana kenan caraf Uwar Gwarama tace"hmm ai  dake tayi sauka Hafizah ce bakaga yadda ƴan unguwa suke zuwa ɗaukar karatu gurinta ba".
"wow masha Allah ashe ƙanwar tawa Malama ce kenan a daɗa bada himma watarana zakiga amfanin abun ".
"insha Allah Yayah".
Hauwah dake gefensu dakyar ta tare dariyar data kusa kuɓucemata tace"muje Uncle Zaid kaga me jikin".
taƙarasa maganarta tana niyyar yin dariya sauke numfashi Zaid yayi danshi har yama manta da abinda ya kawosa lokaci ɗaya yaji wani irin abu yazo ya tsayamasa a zuciyarsa jiyike kamar ya zura da gudu  saboda yadda kansa ke mugun saramasa  dakyar ya yaƙi zuciyarsa gurin cewa"ok muje".
nan tayi gaba yabi bayanta ɓangaren Hauwah ko baƙaramun mamakin su Uwar Gwarama take ba tana wannan tinanin har suka isa ɗakinsu Inteesar.

Suna shiga yaji kansa  ya daɗa juyewa yanajin wata irin muguwar tsanarta na shigarsa a zuciyarsa yanajin inda za'ah bashi wuƙa a lokacin ace ya kashe maƙiyinsa to ba makawa Inteesar ze kashe dakyar ya yaƙi zuciyarsa  ya duƙa yagaida Umminsu Inteesar ba yabo ba

fallasa  ya gaidata Khadijah tagaidashi  a ciki-ciki ya amsa cike da mamakin yadda taji ya amsa gaisuwar Khadijat ta ɗago idanunta  ta kalleshi gani tayi yana bin ko ina na ɗakin da kallon ƙasƙanci da zallar tsana gami da kyama sosai abun yashiga bata mamaki  tana cikin mamakin abinda idonta ke ganemata taji muryar Umminsu tace"Khadijah kawomasa ruwa".
cikin yatsuna yace"a'ah nagode Ummih".
murmushin manya  Ummih tayi suka fice suka barsu  ragewa gurin yayi daka Inteesar seshi a hankali ta miƙe tana tunkaro inda yike abun mamaki setaga  ya miƙe zumbur kamar wanda aka tsireshi da allura ya miƙe yana toshe hanci ya fice waje da sauri dube-dube tashiga yi taga ko ina tsaf yike na ɗakin ba abinda ɗakinsu yike se ƙamshin turare a zuciyarta ta tambayi kanta"to meyasa yake toshe hanci kamar wanda yakejin wari".
rasa me bata amsa ne yasa wata zuciyar cemata "ƙila ƙamshin turaren ne bemasa ba to amma kuma meyasa yake binmu da irin kallon danaga yana binmu dashi ".
rasa me bata amsa ne yasata saurin bin bayansa.

Ɓangaren Zaid ko yana fita ya saki wata nannauyar ajiyar zuciya lokaci ɗaya yaji wata fresh air na shigarsa ya nufi gurin dasu Abbah ke zaune cikin girmamawa ya duƙa a gaban Abbah yace"Abbah ga wannan a siyawa me jiki magani".
washe haƙora Abbah yayi irin na zalamammun iyaye masu tsananin son abun duniya yace"toh!toh!! toh!!! angode Malam Zaidu kaidai baka gajiya  da abun arziƙi angode Allah ya saka da Alkhairi".
"Ameen Abbah ni zan wuce sauri nike".
"toh madallah ka gaida magabatan naka".
"toh  zasuji".
yaƙarasa faɗa yana duben ta inda zeganta caraf suka haɗa ido da Jameelah dake ɗauke da tray a hannunta cikin karairaya take tafiya harta isa  gabansa ta aje tray ɗin dake hannunta haɗe da waro mitsi-mitsin idanunta tace"badai Yayah har zaka tafi ba".
"eh Sis sauri nikeyi  meeting ɗin gaggawa ne ya tasomun".
"okay to amma dai ko   jus ɗin kasha dai".
"anya Sis sauri nike kibari watarana nasha".
kukan shagwaɓa Jameelah tashigayi harta buga ƙafa hakan baƙaramun ƙara burge Zaid yayiba yaƙara lula cikin duniyar ƙaunarta yace"sorry Sis bani insha".
"yauwa Yayana".
nanta zubamasa yasha baƙaramun ɗaurewa kan kowa na gurin yayi Uwar Gwarama tana haɗa ido da Jameelah ta ɗagamata hannu alamun aikinta na kyau nan yayimusu sallama kota kan Inteesar dayaga tana tahowa bebiba ya fice da sauri saurin bin bayansa tayi amma me tana zuwa yana barin gurin a guje ko kulata beyiba zubewa tayi a gurin tare da fashewa da wani marayan  kuka jitayi an dafata tabaya hakan yasata saurin  goge hawayenta tayi saurin ɓoye damuwarta tayi  ta juya haɗe da cewa"Besty  tinanin yadda za'ayi gobe nike narasa meza'ah tarbi ƴan kawo kayannan dashi".
"shine kuma zaki duƙa kamar wadda wani abun ke damunta kodai ƙafar ce ta motsa muje nagama tsara abubuwan da zamu siyo semuyi snacks da drinks se chickens ina ganin ya isa".

"eh ya isa ammafa ni a hannuna befi 6k ba ina tinanin har su sai lemo susai chicken ga uwa uba snacks".
"muje inada kuɗi a account ɗina semuyi amfani dashi".
"toh ke  bakida amfanin da zakiyi dasu da zaki ce ga wasu a gurinki".
"ai Besty ko inada amfanin da zanyi  dashi na fasa meye ranar inada shi ban temakekiba ai abun bemun rana ba haba Besty a tinanina in inada abu tamkar kema kinada shine muje dan Allah musan abunyi".
"hakane kam Besty nagode Allah ya saka da Alkhairi yabarmu tare".
harar wasa Hauwah tayimata haɗe da cewa"ameen Bestyna Allah ya shiryeki Bestyna inban miki ba wazan yiwa".
"Ameen dai Besty".
nansuka shiga dan tsara abubuwan da zasuyi domin tarbar ƴan kawo kaya.

Zaune suke a gaban Boka sun gama zayyanemasa duk abinda ke faruwa tsakanin Inteesar  da Man of the world wata uwar dariya Boka Kutsugu yayi lokaci ɗaya ya haɗe rai tare da cewa"tunkafin kuzo nan nasan da zuwanku wannan yarinyar da kuke gani ba'ah zaune take haka kawai ba domin yarinyar nan da kuke gani ba ƙaramar hatsabibiya bace dole sekinyi da gaske  sannan zaki kamota".
"kinji ko dama na faɗamiki yarinyar nan baƙaramar hatsabibiya bace dama ni ina ganinta  nasan ba haka nan take zaune ba ".
"Boka yanzu ayi duk yadda za'ayi a cire yarinyar nan ta fita daka zuciyarsa asamasa soyayyata a zuciyarsa".
wata uwar dariya Boka kutsugu yaƙara kecewa a karo na  biyu yaƙara haɗe rai ya ɗaga hannu sega wani abu ya bayyana  duk jini a jikinsa me kama da zuciya yana hurawa ya miƙawa Feenerh irin ɗari-ɗarinnan ta riƙa yi da kyankyami ta ansa a yaƙune wai ita me kyankyami aiko garin yaƙuna abu ta sille tafaɗi batt ba aba ba  labarinta dariya Bokan yaƙara yi haɗe da cewa"kinga wannan abar dana baki da kin cinyeta da shikenan kigama da wani Abdallah domin zuciyarsa gabaki ɗaya na ciro na baki kika wulaƙanta".
dafe  ƙirji Feenerh tayi cikin kiɗima tace"kayi haƙuri Boka bansan zuciyarsa bace aida tini na cinyeta dukko da jinin da yike jikinta yanzu ka ƙara bani wata zan cinye yanzu yanzunnan".
"hhh ai aikin gama yarinya ya gama bakin alƙalami ya bushe sau ɗaya muke bada zuciyar ga mutum saura magani na biyu idan kinsamo aikinki zeyi kyau".
wani daɗine ya mamaye zuciyar Zuby ganin aminiyarta tayi loosing ɗin Man of the world hankali tashe Feenerh tace"yanzu Boka ba yadda za'ayi abani zuciyar  yanzu kenan".
"babu zancen zuciya yanzu sede kije ki samo hantar ɓauna kuma ki tabbatar da kanki kika soketa  ki yanko da ita za'ai mahaɗin maganin".
a gigice Feenerh tace"hantar ɓauna kuma Boka nashigesu ni Nafi ina zansamu wata hantar ɓauna  kuma".
wani daɗine yaƙara kama Zuby a zuciyarta tanata farinciki  a fili ko ta nunawa tayi kamar tana alhinin abinda ke damun Feenerh murya na rawa Feenerh tace"Boka  to meze hana nabaka

kuɗi a samo hantar ɓaunar ko nawa kake so a shirye nike dana kashe ko nawane matsawar nidai buƙatata zata biya ".
"hhh ke zaki samo da kanki inba haka ba maganin bazeyi aiki ba dole da kanki zaki nemo".
"toh zan gwada samowa".
"yauwa  ammafa karki kuskure kisa wani ya samomiki akwai matsala gagaruma akan hakan kome yaje ya dawo ki kuka da kanki".
"bama zansa kowa ya samo ba da kaina zansamo".
"yadaifimiki idan kin samo kin kawo dashi zan haɗa miki magani ".
"toh".
nansuka miƙe Feenerh ta aje kuɗin dake hannunta suka fita suka tafi ɗan warewa gefe sukayi da Zuby tace"aiko Ummah dole nakomo gobe ni yabani zuciyar na  cinye sede taji a salansa domin idan nasamu shiga gurin Namijin duniya nunawa zanyi bansanta ba wallahi zan koyawa yarinyar nan hankali seta gane shayi ruwa ne ai Ummah naji daɗi da bata ci zuciyar ba wallahi".
"kibari mukoma gida karta jimu".
"toh".
nan suka tsuke bakinsu suka cigaba da tafiya.

Washe gari tunda ta tashi da asuba bata komaba kamar yadda tasa ba kullum ta share gidan tass tayi wanke-wanke tana gamawa ta nufi gidansu Hauwah!!!!!!!

Votes and Comments
Plz share to others

_*Daga Alƙalamun ƴar Mutanen Gwarzo.*_ƴar Mut🌻 *MAN OF THE WORLD*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK 1*

*PAGES* 3️⃣1️⃣➡️3️⃣2️⃣

Tana cikin tafiya taji muryar Jameelah daka bayanta tana cewa"Aunty Inteesar nima zanbiki ayi aikin dani".
juyawa inda take Inteesar tayi zatayi magsna cikin tsiwa taji Khadijah tace"bama gayya a ƙara gaba ke bama kiji kunyar cewa zaki bita ba saboda ke ɓera ce karfa ki manta itace wadda kuka tsana ɗinnan kuka hanata sakat a rayuwa wadda bakwason ganin cigabanta itacefa wannan karuwar da kuke cewa wadda kuke cewa bawani karatu se yawon tazubar duk wannan be isheku ba saboda ke ɓeran masallacci ce ba kunya bare tsoron Allah kika wani yayimo wani tsumma jikinki wai zaki bita to ba inda zakije bama gayya umma tagaida Ashsha ki ƙara gaba hanyar jirgu daban ta mota daban kuma karki ƙara kiran yayata da Aunty kije can ki nemi Aunty a can badai nanba".
juyawa Jameelah tayi jiki ba kwari saurin kamo hannun ta Inteesar tayi tace"rabu da ita Jameelah kizo muje kekuma banason iskancin banza ko ke tace zatabi da zaki wani sakawa mutane baki taho mutafi bakomai sister".
"nagode Aunty Intee".
"bakomai sister".
"ai gaskiya ce dole infaɗamiki maƙiyinka har abada maƙiyinka ne ko ya zo ya nuna yanasonka ƙarya yike kullum bashi da burin daya wuce yaga bayanka shine saboda ke damo ce sarkin haƙuri mutum yagama takaki yadda ransa yikeso yazo kuma ya shigemiki ki ansheshi lokaci ɗaya ba dolema mutum gobema yaji daɗin hayemiki ba ai yaci ace ki nunamata kurenta koda zaki ansheta".
wata uwar harara Inteesar ta bankawa Khadijah ta kama hannun Jameelah suka shige gidansu Hauwah suka barta nan tsaye baki buɗe ta wuce cikin gida tanata masifa.

Suna shiga suka samu su Hauwah dasu Momynta sun kammala aikin snacks ɗin har sun fara celling ɗinsu da raping sheet turus tayi haɗe da kama haɓa ta ware fararen sexy eyes ɗinta tace"badai har kun gamaba Momy".
hararta Hauwah tayi tace"da jiranki zamu tsaya yi ne alanƙosa aida mun tsaya jiranki da ƙila sede muji kunya domin ke ɗinnan yadda kike da nawa ina tinanin a gidanki Uncle Zaid zesha fama dake".
damm ƙirjin Jameelah yabayar sakamakon tinowa datayi yau za'ah kawo lefen Zaid da wata bada itaba har yau be kirata ya sanarmata da yanason ta ba tana cikin wannan tinanin taji muryar Inteesar cikin shagwaɓa tace"Momy kinji Hauwah tana cemun wai alanƙosa".
murmushi Momy tayi tace"rabu da ita ƴar albarkana itace alanƙosa domin itama yanzunnan fitowarta kenan ta zauna ba abinda takeyi se aikin ci daka ni se Hindatu mukayi aikin komai

kuma ma inban dage na fitar da ɗiyata kunya ba wazan fitar rabu da ita".
gwalo Inteesar tayiwa Hauwah haɗe da cewa"muje Jameelah".
"toh Aunty".
nan suka tafi sosai su Momyn Hauwah suka yi mamakin ganin Inteesar da Jameelah amma sesuka make zama suka yi suka tayasu raping ɗin kayan suna gamawa Inteesar tace"Jameelah ki iba ki ɗanɗana".
"toh Aunty".
nanta ɗauki komai ɗaya taci itama Inteesar ta ɗauka ta ɗanɗana suka taya Hindu me aiki kai kayan cikin gida bayan sun gama kamar gaske Jameelah tace"Aunty bara naje gida na shirya tunda naga har angama aikinma".
"toh sis".
nanta fita sukuma suka nufi ɗakin Hauwah suna shiga suka zauna kan ɗan madaidaicin gadon Hauwah taɓa Inteesar Hauwah tayi tace"wai Besty ya akai naganki da wannan yarinyar ne".
"wacce yarinya fa".
"hmm gaskiya Besty rainin hankalinki yawa ne dashi wacce yarinya nike nufi bayan Jameelah naga yarinyar nan ba wadda ta tsana sama dake kika wani jawomana ita ke bakya tinanin ko turota akayi dantaga abinda mukeyi ba".
"hmm keda Khadijah kuna bani mamaki wallahi na taho zanzo nan gidan yarinya tacemun zata bini so kuke na koreta shi ɗan adam ba'ah masa haka bakasan ranar da zemaka ba shi ɗan adam rana garesa ko biki taɓa karanta littafin marubuciyar nan ba Real eeshow mesuna BAR RAINA ALLURA (Itama ƙarfe ce) labarin ya ƙayatar dani sosai saboda marubuciyar ta nuna duk yadda mutum yakai da ƙinka a rayauwa be isa ya hanaka samun rabonka ba duk ƴinshi dakai ita rayuwa haka take zakaga kaƙi mutum ƙarshe shiɗin dai daka raina gaba shize temakeka gaskiya zan turomiki da littafin ki karanta zaki faɗakantu sosai labarin Sajida duniya ne".
"eh dai naji amma kinsan wani abu idan kika cigaba da wannan haƙurin naki mutane zasuyita cutarki saboda yarinyar nan da uwarta inda za'ah basu wuƙa ace su kashe wani abu da suka tsana wallahi ke zasu kashe  nifa na tsanesu wallahi".
"dan Allah mubar wannan zancen batashi nike ba tin jiya narasa gane kan Zaid tunda yabar gidanmu na kirashi ya ɗaga ko magana be bari nayi ba yacemun wai aiki yikeyi idan yagama ze kirani  shiru-shiru inata jira ya kirani be kirani ba dana daɗa kiranshi be ɗauka ba har zuwa yau idan na kirashi baya ɗauka na biki yadda nikejin zuciyata ba na riga na saba da waya dashi wallahi jiya se wajen huɗu bacci ya ɗaukeni hankalina har yanzu yaƙi kwanciya wallahi".
dariya Hauwah tayi ta kama baki tace"oh su Besty anyi nisa ba'ah jin kira wannan irin ƙauna haka harda ƙinyin bacci lallai Uncle ɗina ya iya love irin wannan mutuwa haka da kikayi kansa haka sefa kina mishi uzuri tunda kinsansu masu kuɗinnan sunada sabgogi a gabansu bare kuma satin biki yakama dole sekinmasa uzuri romeo".
"eh najin inban damu da mijin dazan aura ba wa kikeso na damu dashi amma aida baya iya bacci har seya yimun addu'ah na kwanta sannan muke sallama a waya shiyasa jiya nakasa bacci".
"hhh dole Besty ki kasa bacci tunda yariga yagama shagwaɓaki dole kice kinkasa bacci niko Allah muntuba aini gani nike ba'ah yo mutumin dazan kasa bacci ba dominsa ba gaskiya".
"hmm haka dai kikace dandai har yau baki haɗu da wanda kike so bane shiyasa wayasanma ke me zaki gwarama ni anga nawa".

"hhhh".
nan suka cigaba da hirasu  da ƴan tsare-tsaren ansar kaya.

Kwance yake akan tamfatsetsen italian bed ɗinsa idanunsa a lumshe kamar me bacci tsaki yayi haɗe da buɗe sexy eyes ɗinsa yace"anya ko wannan yarinyar  ba mayya bace ba kuwa meyasa dana rife ido ba abinda nike gani se ita gaskiya inko ba mayya bace ƙila ta haɗa iri dasu take ƙoƙarin cinyeni koma dai menene Allah yafiki stupid kawai".
ƙara sakin wani tsakin yayi yaƙara lumshe idanunsa nanma still ba abinda yike gani se ita tsaki yaƙara yi yaji an turo ƙofa anshigo wasu english wears ne jikinta wando da riga wandon iyakarsa guiwarta jeans baƙi se rigar sky blue me ratsin net daka gurin ƙirjin baƙaramin kama jikinta kayan sukayi ba tasha uban kitson atarch har ɗuwawu tana tafiya ko ina na jikinta na motsawa  hannunta ɗauke da cup ɗin coffe jikin drawer ta nufa da niyyar aje coffeen dake hannunta caraf idanunta ya sauka kan faffaɗan ƙirjin Abdallah dake cike da gashi irin na jaruman maza masu ji da class se ɗaukar ido gashin keyi shedar yana shan gyara tana ajewa ta juya idanunta ya rife ta kai hannu da niyyar taɓawa taji ya dakamata tsawa haɗe da cewa"ke wacece irin tinkiya ce mara tarbiyya waya baki izinin shigomin part  da har kika wuce falo kika shigomin bedroom with out my permission dakin bari wannan ƙazamun hannun naki ya taɓamun jiki da sekin  raina kanki domin wallahi da sena nunamiki true colour ɗina ".
sosai yayimata kwarjini lokaci ɗaya ta diririce murya na rawa tace"dama Yah Abdallah coffee na haɗomaka".
batare daya buɗe sexy eyes ɗinsa ba yace"nacemiki ina buƙata ne da zaki shigowa mutane bedroom bako sallama saboda rashin hankali ko da ke kike bani coffee  ɗin ko ancemiki ni inashan coffee ɗin kowanne tom and jerry ne irinki kinfice da tsiyarki kinbani guri ko sena tashi stupid kawai mara aji".
saurin ɗaukar coffen ta tayi jiki na rawa ta fice tana fita yayi tsaki ya miƙe tare ɗaura towel ya nufi toilet.

4:00pm
Hauwah na shirin shiga gidansu Inteesar wasu haɗaɗun motoci guda huɗu suka yi parking biyu hilux biyu Parado baƙaƙe se ɗaukar ido suke parking suka yi daidai ƙofar gidansu Inteesar wasu haɗaɗun matane dattijai wanda bazasu gaza shekaru 50 ba suka fito daka mota ɗaya su biyu amma inkagansu seka ɗauka ƴan shekaru talatin da biyar ne saboda yadda jikinsu ya nuna kana ganinsu kasan sun jiƙu da naira  ɗaya motar kuma wasu matane su huɗu matasa masu jini a jika suka fito masu tsananin kama da Zaid musamman ma ƙaramar cikinsu sauran hilux ɗin biyu kuma shaƙe suke da akwatuna wani daɗine yakama Hauwah ta nufi inda suke cikin girmamawa tace"Ina yininku".
"lafiya ƙlau badai kishiyar tawa bace daiko data kwacen miji na bace ko" .

cewar ɗaya daga cikin dattijan dariya Hauwah tayi tace"Babah ba ita bace ƴar uwarta ce ita tana can gidan".
tafaɗa ta me nuni da gidansu  sosai taji daɗin jin wannan kalaman daka bakin wannan matar hakan ne yaƙara tabbatarmata da dangin Zaid suna son aminiyartata  nan tayimusu jagora zuwa cikin gidan  ɗaya daga cikin matasan matannan ce tace"amma dai sister zaki kaimu inda amaryar tamu  take ko".
"insha Allah zankaiku".
"yauwa Jabeer ku shishigo da kayan ".
"toh ranki shidaɗe".
cewar Jabeer nan suka shige gidansu Inteesar .

Bayan sun gama gaisawa ne su Jabeer suka fara shigo da haɗaɗun akwatuna seda suka shigo da akwati sha biyu nan aka shiga buɗa akwatunan dake shaƙe da kaya  tsadaddun kayane ƴan ubansu a ciki kowanne da takalminsa da mayafinsa da jakarsa sosai murna gurinsu Khadijah da Hauwah ba'ah cewa komai tun suna ƙirga kaya har suka dena domin Zaid yayi ƙoƙari sosai nan Momynsu Hauwah tasa su Hauwah su fito da snacks ɗin da sukayi aka aje a gabansu  da kuɗin tukuicin da Abban Hauwah ya bayar dubu goma aka  basu har an aje akasa aka kaisu mota Hauwah tayiwa wannan budurwar rakiya zuwa gidansu suga Inteesar .

Kwance take tana karatu littafi taji shigowarsu Hauwah ba tare data  tashi daka inda take ba ta amsa sallamar su Hauwah  shiga sukayi suna shiga ƙanwar Zaid a zuciyarta tace"wow gaskiya dole bro ya gigice amma gaskiya ta haɗu ko ni mace nasan ta haɗu balleshi da yike namiji kalli gashinta dan Allah har gadon baya".
tana cikin zancen zucin taji Hauwah tace"Besty ga ƙanwarki tace tana son taga wadda ta susutamata Yayanta".
rife fuska Amna tayi tana dariya tace"Aunty ina yini".
murmushi Inteesar tayi tace"lafiya ƙlau Amna ko".
ɗagamata kai tayi bayan sun gaisa suka kawomata ruwa tasha suka ta miƙe nan suka mata rakiya a bakin get ɗin gidansu Hauwah Inteesar ta tsaya tare da ɗagamata hannu alamun bye-bye sannan ta juya.

Ɓangaren Uwar gwarama ko tunda taga irin  dukiyar da  Zaid ya kashe a lefen Inteesar hankalinta yaƙara tashi takasa zaune takasa tsaye ko gurin lefan  bataje ba saboda tsananin baƙin cikin dake damunta ga Jameelah ta tasata a gaba se kuka takemata kan ita har yau bataga alamun Zaid baze auri Inteesar ba hankalinta inyayi dubu ya ɓaci ta rasa inda zata saka

kanta taji daɗi.

Washe gari  suna tashi suka tafi gurin aiki da wurwuri suna isa Comphanyn kowacce ta nufi gurin aikinta a hankali take tafiya kamar kazar da kwai ya  fashewa a ciki yayinda zuciyarta ke dukan uku-uku  sakamakon tayi fashi bata sanarmasa ba a hankali ta tura ƙofar office ɗinsa yayinda zuciyarta tashiga bugawa da sauri -sauri kanta a ƙasa tashiga!!!!!!

_*Ga meson karanta book two ɗin MAN OF THE WORLD nafara post ɗinsa a paid group ɗina domin book two na kuɗine  akan farashi mafi sauƙi naira #300 domin neman ƙarin bayani ki tuntuɓi wannan number koda kuɗinka seda rabonka 08108362334.*_

Votes and Comments
Plz share to others

_*Daga Alƙalamun ƴar Mutanen Gwarzo.*_anen Gwa🌻 *MAN OF THE WORLD*
(NAMIJIN DUNIYA)

*MALLAKIN*
*REAL EESHOW*

HOME OF QUALITIES WRITERS ASSOCI…

*BOOK 1*

*PAGES* 3͏3➡️3️⃣4️⃣

Samun office ɗinsa tayi bakowa a ciki se ƙarar a.c dake ta faman aiki da mayataccen ƙanshin turarensa daya kama office ɗin waige-waige tashiga yi gani tayi bataga alamar yazo ba sosai tayi mamakin rashin zuwansa  da wuri domin tasan yana rigata zuwa duba agogon dake

ɗaure a tsintsiyar hannunta tayi taga har goma tayi zuciyarta ce tacemata"ke meye naki na damuwa dan wannan mara mutuncin bezo ba aikyama fi sakewa da binki da yikeyi da wa'innan mayun idanun nasa masu firgita mutum".
tana gama faɗin haka a zuciyarta ta taɓe ɗan ƙaramin pinky lips ɗinta ta wuce toilet tashiga aikinta tana gama wankin toilet tashiga goge chairs and tables ɗin dake cikin office tana gamawa ta share ko ina fes ta gyara ko ina yazama neat ta nufi gurin zaman sakatariya ta zauna ta shiga duduba takardun dake kan tables ɗin kamar an tsikareta ta miƙe tare da kallon tamfatsetsen agogon dake manne a office ɗin ta nufi cikin office ɗinsa tana shiga ta nufi drower dataga room freshners ta ɗauki ɗaya daga cikinsu tashiga fesawa ko ina na gurin ta wani toshe hanci tana cikin mitarta Hauwah ta shigo bakinta ɗauke da sallama amsamata tayi ta cigaba da fesa room freshner ɗinta ƙarasawa inda take Hauwah tayi tare da cewa"Besty wai yanaga kinata faman toshe hanci sekace wadda taji wari bakiji yadda kika cika room freshnern nanba har hawa ka yikeyi ".
"ai warinne domin turaren wannan mutumin har hawa kai yikeyi sabo da rashin daɗin ƙamshinsa har tasarmun da zuciya yikeyi wallahi inji kamar zanyi amai ".
"hhh Besty banda dai sharri dandai kuna faɗa dashine shiyasa kika tsaneshi amma ai Sir Abdallah komai nasa na daban ne ni tunda nike bantaɓa jin irin ƙamshin turarensa jikin wani kinsanfa shiɗin duniya ne ".
taɓe baki Inteesar tayi haɗe da cewa "Besty Allah bazancen sharri bakuma tsanarsa nayi ba kawai halinsa na tsana na girman kai da ɗagawa da nuna shi wanine uwa uba rashin tarbiyya da rashin ganin girman nagaba dashi ko kunya bayaji mutanen da suka girmesa suyita duƙawa suna gaishesa sekiga seya ɗauki lokaci saboda isa da izza sannan ze amsa wa'innan halayen nan nasa na mugun ɓatamun rai wallahi shi ko kunya bayaji isa kamar wani basarake".
"hhh ni banga wata izzaba kedai kawai dan bakwa shiri dashine shiyasa kike ganin kamar bashi da kirki amma Sir Abdallah yanada kirki sosai ga sanin yakamata".
zaro sexy eyes ɗinta tayi haɗe da cewa"wannan mutumin ne yasan yakamata tabɗi a rashin samun wa'inda suka san yakamata ƙila a ɗaukeshi domin wannan mara tarbiyyar mutumin ko hanyar inda yakamata tayi bebi ba".
"to maida wuƙar bani nakar zomon ba rataya aka bani Besty ba wannan yakawoni ba gani nayi har 12pm tayi so nike yau mutafi da wuri saboda mufara tsare-tsarenmu ina tinanij daka yau ba lallai bane muƙara zuwa office ba inaso a gyarawa Uncle Zaid ke sosai dan karya rainamun ke ".
"dama nima yanzu nagama tinanin hakan yau tunda na tashi gabana keta faɗuwa na rasa dalili kome yake faruwa oho jinike kamar wani abu ze faru dani".
" insha Allahu Besty ba abinda ze faru dake se Alkhairi kinji Bestyna kedai kawai idan kinji haka ki riƙa Innalillahi wa'innah ilaihi raji'un ki yawaita addu'ah wajan biyu zamu tafi kisan dabarar da zakiyiwa Sir Abdallah".
sauke numfashi Inteesar tayi cikin sanyin murya tace"nagode Bestyna Allah yabarmu tare keɗin mahaɗin rayuwata ce Besty kinmun komai na rayuwa kullum baki da burin daya wuce kisani farinciki Besty nagode da kulawarki gareni Allah nima kabani ikon temakon wannan baiwa taka ".
taƙarasa zancenta hawaye na niyyar zubowa daga lulu eyes ɗinta girzgizamata kai Hauwah tayi alamun kar tayi kuka tace"Besty banason godiyar nan da kikemun domin nasan inke kike da

damar da nike da ita  da ba abinda bazakimunba toni meyasa bazan mikiba bayan inada halin yi domin keɗin kin wuce ƙawa a gareni ƴar uwata ce dan Allah duk abinda zanmiki kidenamun godiya".
saurin rungumeta Inteesar tayi haɗe da fashewa da kuka seda sukayi kuka me isarsu sannan suka saki junansu Hauwah tace"Besty bara na koma gurin aiki".
kai kawai Inteesar ta iya ɗagamata  saboda kukan datasha nan Hauwah ta tafi tabarta jiki bakwari ta koma mazauninta na sakatariya a zuciyarta tana mamakin rashin zuwan Namijin duniya.

"gaskiya Ummah kayannan kwata-kwa basu dace da wannan tsinanniyar yarinyar ba da Jameelah suka dace".
"haba Saratu ya kike irin wannan ne  ke ai da Jameeha da Aishatu  duk ɗaya ne   meye abun baƙinciki kowa rabonsa ze samu kidena irin wannan ke babbace memakon kizama me kwantar da fitina seki zama me tayar da ita".
a harzuƙe Uwar Gwarama tayi kan Badi'ah tana huci tace"nace duk biyune karki ƙara haɗamun hafizar  ƴata da wannan ƴar barikin yarinyar data gama zubar da mutuncinta a titi ai gaskiya Saratu ta faɗa  ai kozan rasa zanin ɗaurawa bazan taɓa bari ɗiyar Amina tayi aure inda zata hutaba kozan rasa koda zanyi yawo tsirara senaga bayanta daka ita har shegun ƴaƴannan nata masu yawon bariki anyako nina haifi wannan salamammar kuwa ni Hajara da a asibiti na haifeki da se ince canzamun ke akayi salamammar banza wadda batasan ciwon kanta ba kika ƙara sakamana abiki wallahi akan maganarmu wallahi sena saɓamiki shegiya ƴar uwartaki kikewa baƙinciki sarkin baƙin ciki kawai me baƙin halin tsiya kawai ".
jin furucin mahaifiyarta ne yasata kama bakinta  tayi shiru taji Uwar Gwarama  tace"kwantar da hankalinki ƴar albarka meson ganin farincikina wannan lefe da kike gani ba makawa na Jameelah ne kedai kawai ki zuba ido kisha kallo duk wannan ɗan banzancin da sukeyi zasu koma suyi laƙwas dani suke zance ni kaina nasan bani da kyau".
cikin zumuɗi Saratu tace"Allah Ummah  kice mufara shirin shiga aljannar duniya kenan".
"sosaima kuwa tawan ki kira su Hafsah ki sanarmusu suma su shirya".
"nagode Mamana  takaina Allah yabarmana ke".
"Ameen dai  tawan".
Uwar Gwarama tafaɗa ta wurgawa Badi'ah harara  shiru  tayi suna nan zaune sukaji sallamar Inteesar saurin miƙewa Badi'ah tayi ta fita tsaki Uwar Gwarama tayi haɗe da cewa "sakarai kawai wadda batason ciwon kanta ba kinga ai taji sallamar uwarta har jikinta ke ɓari dan taje gurinta karta tsinemata narasa me Aminah tayiwa Badi'ah ta liƙemusu haka ba".
"ai Ummah aikin asirine wannan kiga dan Allah yadda har jikinta ke rawa kamar mazari dakajin muryar waccan karuwar".
"aiko nafi ƙarfinta wallahi ".
nan Saratu taita zuga Uwar Gwarama.

Da fara'arta tace"nayi fishi sis shine kinsan da zuwana kikayi tafiyarki aikinki".
saurin kama kunne Inteesar tayi alamun bada haƙuri tace"tuba nike babbar yaya nina isa inyi tafiyata inbarki zuwa dai nayi saboda daka yau bazan sake zuwa ba aikuma na dawo da wuri".
"da wasa ma nike sis  ɗina kinsan bazan taɓa fishi dake ba tawan naga lefe Allah yasanya Alkhairi yabaku zaman lafiya".
a zuciyarta ta amsa a fili kuma ta rife fuskarta alamun kunya  dariya Badi'ah tayi tare da kama hannunta suka nufi ɗakin Ummi wani ɓangare na zuciyar Inteesar ko ba abinda take son ji se dalilin daya hana Man of the world ƙin zuwa gurin aiki ta rasa me bata amsa  tambayarta hakan yasata saurin kautar da tinaninshi suka cigaba da hira da ƴar uwarta.

Cikin sauri-sauri yake sakkowa daga step!!!!!!!!

1-Meyasa Inteesar take yawan faɗuwar gaba?
2-Waye ke sakkowa daga step yana sauri?
3- Jameelah zata auri Zaid kuwa?
4-Man of the world ze tafi da Inteesar  UK kuwa  zata yadda tabishi kuwa?
5-Aikin boka zeci Zaid kuwa ?
6-Meye asalin maman Inteesar da ake ganin kamar bata da asali?
*Domin jin amsoshin waɗannan tambayoyin kibiya ki karanta cikin salama kuma inkinsan zaki siyane danki fitarmun dan Allah karki siya.*

_End of book one meson jin yadda zata kaya tsakanin Man of the world da Inteesar ya biya #300 Normal grp, vip # 800 , pc 1k  ɗinsa ta wannan account number 2411022356 Aisha Umar Ibrahin Zenith Bank aiko da shedar biyanka ta wannan number 08108362334_

_*Daga Alƙalamun ƴar Mutanen Gwarzo.*_rzo.*_